
# Yi Gini Cikin Mutuncl Dokokin Ɗa’a na Meta

Wani ginshiƙi na tabbatar da mutane cikin tsaro da kuma yin wani kyakkyawan tasiri




Meta



# Abubuwan da ke Ciki

03 **Gabatarwa**

04 Wani saƙo daga Mark Zuckerberg

05 Ƙa'idojinmu ginshiƙai ne ga Meta

10 **Taimakon Juna**

11 A rungumi bambance-bambance, adalci da tafiya da kowa

13 Kasance mai kirki da girmamawa

15 Ka samar da muhallin aiki mai tsaro

17 Zama mai biyayya da gaskiya

20 Kare bayanan sirri na Meta

23 Kare kadarorin Meta

25 **Karewa da Ƙarfafa Jama'a**

26 Kafa al'adar mutunta bayanai a ɗaukacin Meta

28 Yi gini cikin mutunci

31 A kare dandalin biyan kuɗi

33 **Yin gasa tare da Haɗaka**

34 Bi dokokin kasuwanci na duniya

36 Yi gasa cikin ƙwazo da adalci

38 Yi haɗaka cikin mutunci tare da wasu daban

41 **Mu'amala da Duniya**

42 Kasance abin koyi wajen tsare gaskiya a harkar kuɗi

44 Kada ka shiga a cinikayyar yankan baya

46 Ka yi sadarwa a bayyane tare da faɗin gaskiya

48 Ka hana cin hanci da rashawa

51 Bayarwa da karɓar kyaututtuka da nishaɗantarwa

53 Ka yi mu'amala da gwamnati da shugabannin siyasa cikin mutuntawa

55 Samar da duniya mafi nuna kulawa, mai ɗorewa

58 Wasu Sassa na biyayya da kuma Dokokin Ɗa'a

59 Cimma manufarmu cikin mutuntawa, alhakin kowa da kowa ne

# Dokokin Ɗa'a na Meta: Ku taimaka mana mu yi gini cikin mutunci



## An kafa meta ne don cimma wata muhimmiyar manufa: don ta ba wa mutane wani iko su gina al'umma su kuma jawo mutanen duniyakusa da juna.

Akwai buƙatar mu ja ɗamara wajen aiki tuƙuru da kuma tsare dokoki saboda irin tasirinmu da kuma jama'a da muke cimma, mu tabbata mun samar da kayayyaki da tsare-tsare da ke da kyakkyawan tasiri ga jama'a, mu ba jama'a kariya tare da kula da kowa.

Dokokin Ɗa'a su ne ginshiƙinmu. Suna taimaka wa duk wanda yake aiki a Meta don ya fahimci nauyin da ke kanmu su kuma ƙarfafe shi da ya yi aiki cikin mutunci. Yana bayyana wasu dokokin da suka zama wajibi mu yi biyayya gare su da kuma manyan tsari da muka ɗora wa kanmu. Duk da bai shafi kowane yanayi da za ka iya fuskanta a aikin yau da kullum ba, ya kamata Dokokin Ɗa'ar su zama mahangar ka ta farko duk lokacin da ka fuskanci wata shawara mai wahala ko ɗaure kai.

# Wani saƙo daga Mark Zuckerberg

A Meta, muna gina kayayyaki da sabo domin bai wa mutane ikon gina al'umma da kuma jawo duniya kusa da juna.

Da wannan ne ake samun matuƙar kula da juna, da kuma al'ummar da muke yi wa aiki da duniya baki ɗaya. Na yi amanna cewa rungumar wannan nauyin kan ba mu damar ƙirƙira - kuma mu kasance kamfani na gari.

Waɗannan Dokokin Ɗa'ar suna fasalta abubuwan da muke tsammani na yadda muke aiwatarwa da yadda muke yanke shawarwari. Wajibi mu duba su a duk lokacin da muke da wata tambaya ko fuskantar daidaitawa da ko abubuwa da suka shige duhu.

Muhimmancin aikinmu yana nuna cewa dole dukkanmu mu sa himmar ɗora wa kanmu aiki da Babban tsarin aiki. Don haka nake son ganin kowa a Meta—shugabanni, manajoji, ɗaiɗaikun masu ba da gudummawa da ma'aikatan wucingadi da su bi Dokokin Ɗa'armu, su wayar da kan saura su ma su bi, sannan su sami ƙwarin gwiwar yin magana idan kana buƙatar taimako ko kana da tambayoyi.

Bari mu yi amfani da wannan Dokokin Ɗa'ar mu yi gini cikin mutunci.

Mun gode,

Maki

# Ƙa'idojinmu ginshiƙai ne ga Meta

An samar da Dokokin Ɗa'ar ne daga ƙa'idojinmu, kuma su ne abubuwa da muka yi imani da su muka riƙe su hannu bibbiyu. Suna taimaka mana wajen yadda muke yanke shawarwari a kowace rana.



## Ƙa'idoji biyar su ke jagorantar aikinmu a Meta:

1 Muna ba jama'a damar yin magana—muna samar da kayayyaki da tsare-tsare don haka kowa yana da damar yin magana—don ba da labarinsu, su rarraba, su haɗa, don a ji su kuma su canja rayuwarsu da kyau.

2 Samar da haɗin kai da al'umma—saboda mun yi amanna da ƙarfin jama'a idan suka haɗe wuri ɗaya, mun mayar da hankali wajen taimakawa mutane su haɗu da juna.

3 Yi ma kowa aiki—idan ka yi amanna da ƙarfin jama'a, akwai buƙatar ka tabbata ka samar da damarmaki iri ɗaya ga kowa.

4 Ka ba jama'a tsaro da kuma kare sirri—mun mayar da himma wajen kare al'ummominmu daga cuta.

5 Bunƙasa ayyukan tattalin arziki—jama'a na amfani da kayayyakinmu a kowace rana don su haɗu waje ɗaya su gano wata dama ta tattalin arziki don cigaban rayuwarsu, a tsakanin al'ummominsu ko kuma ƙungiyoyinsu.

# Ana son kowa da kowa daga cikinmu da mu riƙe Dokokin Ɗa'a da kyau

Waɗannan Dokokin Ɗa'ar su ne ginshiƙai game da yadda muke aiki tare da samar da tasiri a duniya, da kuma yadda muke ɗaukar alhakin raya ƙa'idojinmu—yana da muhimmanci.

Dukkan ma'aikatan Meta—tun daga shugabanni har zuwa masu koyon aiki—dole ne su bi kuma su riƙe Dokokin. Saɓa wa dokar zai iya jawo a ɗauki matakin ladabtarwa, har zuwa kuma haɗi da kora daga aiki ko jinga da kuma sakamakon biyan kuɗi.

Doka r ta shafi:

| MASU SAURARO | MA'ANA | KEƁAƁƁUN KALMOMI DA AKA YI AMFANI DA SU A ƊAUKACIN DOKOKIN |
|---|---|---|
| Meta | Dukkannin Meta, haɗl da dukkan rassa da ɓangaririnmu da ke faɗin duniya (m.s.,Meta Ireland, Instagram, WhatsApp, d.s.) | Kamfanin Meta |
| Ma'aikatan Meta | Mambobin Hukumar Daraktoci, jami'ai, da ma'aikatan Meta, da ma'aikatan wucin gadi (da suka haɗa da ma'aikatan dillanci, masu kwangila da 'yan kwangila masu zaman kansu) | Ma'aikatan Meta<br>"Mu" ko "mu" ko "Namu" ko "Junanmu" |

# Abubuwan da ake Buƙata daga ma'aikatan Meta

## Ana buƙatar Dukkan Ma'aikatan Meta su:

- Yi aiki bisa dokoki da ƙa'idojin Meta kuma su bi abubuwan da ake nema a wannan Kundin Dokoki da manufofin Kamfani.
- Su yi aiki a kan doka, gaskiya, da kyawawan ɗabi'u don cimma muradun Meta da kuma masu amfani da Meta a dukkan lokuta.
- Kammala horon da ake buƙata, yi amfani da Dokokin Ɗa'a sannan kuma ka yi magana a duk lokacin da kake da wata tambaya ko wata damuwa.
- Cikakken Haɗin-guiwa da binciken Kamfani, da suka haɗa da abubuwan da kae bukata a tattare da ƙarfin guiwa, halarta da kuma gaskiya.
- Kada ka yi ramuwar gayya a kan dukkan wanda ya nuna wata damuwa da kyakkyawar manufa ko kuma game da yiwuwar saɓawa Dokokin Ɗa'a, manufofin Meta ko doka, ko kuma wanda ya bayar da haɗin kai ga wani bincike.

## Haka kuma, Ana buƙatar waɗanda suke jagoranci ko kula da Meta su:

- Ka zama kyakkyawan misali, ta sanin cewa halaye da shawarwarinmu suna tasiri ga wasu, da ya haɗa da ta rungumar muhimmancin bin Dokokin Ɗa'a da manufofin Kamfani.
- Samarwa tare da tattala kyakkyawan muhallin aiki inda kowa ke jin ana yi da shi sannan aka ƙarfafa masa guiwar yin abin da ya dace kuma ya yi magana a lokacin da yake da ra'ayi, martani ko damuwa – wannan na nufin a saurari tambayoyi da ƙorafe-ƙorafe da kuma ɗaukaka lamari idan akwai buƙatar hakan.
- A gaggauta kai rahoton yunƙuri ko saɓa wa doka ko wannan Dokokin Ɗa'ar ko ƙa'idojin Kamfani.



# Yin magana da samun taimako

## Maganarka na da matuƙar muhimmanci.

Yin magana na da muhimmanci idan ka ga ko ka yi zargin saɓa doka, wannan Dokar Ɗa’a ko wata daga manufofin Meta. Ba dole ba ne sai ka samu dukkan bayanai ko cikakken bayani kafin ka yi tambayoyi ko yin magana.

Ka yi tambayoyinka hankali kwance ko kai rahoton wata damuwa ta amfani da duk wata kafa ko kayayyakin aiki da suka kwanta maka a rai. Ka gasgata cewa za a ɗauki tambayoyinka ko damuwarka da muhimmanci sannan a magance su nan take a asirce.

## Ko da yaushe za ka iya kai damuwarka ga:

- Manajanka ko wani manajan
- Hukuma ko wani mamba na tawagar Ɗabbaƙawa da Ɗa’a
- Masu Samar maka da Ma’aikata (HR) Abokan Huldar Kasuwanci
- Mai Kula da Hulɗar Ma’aikatanka
- Mai Bincike na Cikin Gida
- Don damuwar da ke da alaƙa dasirri, **Kayan Aikin Kai Rahoton Sirri**
- Haka kuma za ka iya miƙa rahoto ta hanyar Yin Magana, Tsarin Meta na kai rahoton damuwa, wanda yawanci yake ba da damar yin rahoto ba tare da suna ba:
  - Ziyarci **fb.integrityline.com**
  - Kira **+1-877-564-9619**
  - Dannan lambobin samun dama kai tsaye da suke **business.att.com/collateral/access.html** sannan +1-877-564-9619 sai ka bi umarnin mai gudanarwa
- Ga Ma’aikacin Wucingadi, ta hanyar ɗaukaka matsala ta kamfaninka da kuma ko hanyar tuntuɓa ta HR (POCP)

Domin ƙarin bayani a game da kayayyakin aiki da kuma zaɓin kai rahoto a ɓoye, ziyarci **Dokar kai Koke da Kwarmato**.

Idan kana da tambayoyi game da Dokokin ko kana buƙatar wani batu na daban ko ba ka da tabbas game da yadda za ka kai rahoton damuwa, to ka ziyarci **Ɓangaren Ɗabbakawa da** Ɗa’a (don FTEs) ko portal ɗin mutane shafin Ma’aikatan Wucingadi ko **CWquestions@** (don CWs) don samin tallafi.

## Abin da zai faru nan gaba: ayyukan bincike

A duk lokacin da Meta ya sami labarin yiwuwar saɓa doka, wannan Kundin Dokokin ko duk wasu manufofin Meta, Kamfanin zai ɗauki mataki. Wannan yawanci ya haɗa da yin cikakken bincike, na gaskiya da adalci. Meta zai yi duk wani ƙokari na sauararon dukkan ɓangarorin da lamarin ya shafa cikin lokaci, ba tare da nuna bambanci ba da kuma sirrantawa daidai gwargwadon hali tare da bin dokokin da suka dace.

Don tabbatar da cewa za mu iya gudanar da bincike mai amfani, an wajabta maka shiga binciken kamfani idan an nemi haka, yin biyayya ga buƙatun sirrantawa da kasance mai gaskiya da amana, tare da bayar da gamsasshiyar amsa ga tambayar da aka yi.

Idan muka gano cewa saɓawar ta auku ko kuma wani bai da gaskiya a lokacin gudanar da bincike, za mu ɗauki mataki da ya dace, har ma da matakin ladabtarwa har zuwa kora daga aiki da sakamakon biyan kuɗi idan da yiyuwa ma, a tura ga hukumar jami'an tsaro.

## Ba za a yarda da ramuwar gayya ba


Yin magana ba abu ne mai sauƙi koyaushe, amma kuma shi ne abin da ya dace a yi da kuma abin da muke so ke nan a Meta. Wannan ne ya sa a ƙarƙashin **Dokar kwarmato da Ƙorafi**, ba ma yarda da ramuwar gayya a kan kwane mutum da:

- Ya kai ƙorafin wata damuwa da kyakkyawar niya game da saɓawa doka, wannan Kundin Dokokin ko manufofin Kamfani, ya bayyana niyyar yin haka ko kuma ya taimaka wa wasu Ma'aikatan Meta wajen yin hakan
- Shiga cikin wani bincike

# Yin aiki tare da Tawagar Ɗabbaƙawa da Ɗa'a a Meta

Tawagar Ɗabbaƙawa da Ɗa'a wata abokiyar hulɗa ce ga kowa a Meta don daidaita sarƙaƙiyar yau da kuma hasashen masu zuwa a gobe.

Ziyarci **Cibiyar Ɗabbaƙawa & Ɗa'a** don samun kayan aikin da hanyar tuntuɓa don ɗabbaƙawa da jagoranci a kan yadda za ka yi hukunci cikin mutunci a Meta. Kada ka yi jinkirin yin magana da tawagar Ɗabbaƙawa da Ɗa'a don samin tallafi.



# Yin gini cikin mutunci tare da juna

## Don samar da mahaɗa da gina al'umma, dole ne mu fara aiwatar da irin wannanacikinal'ummarmu ta cikin gida



### A wannan sashen:


| | |
|---|---|
| A rungumi bambance-bambance, adalci da tafiya da kowa | 11 |
| Kasance mai kirki da girmamawa | 13 |
| Ka samar da muhallin aiki mai tsaro | 15 |
| Zama mai biyayya da gaskiya | 17 |
| Kare bayanan sirri na Meta | 20 |
| Kare kadarorin Meta | 23 |

# A rungumi bambance-bambance da adalci da tafiya da kowa

Mun himmatu wajen samar da mabambancin wurin aiki na bai ɗaya inda kowa zai san ana damawa da shi sannan kuma an ƙarfafa musu wajen nuna hazaƙarsu a wurin aiki.

Hakan zai ba su damar ba da gudunmuwar fasaha, hikima da tunaninsu cikin ‘yanci. Za mu iya daidaita bambancin tunaninmu don samar da kayayyaki masu kyau da yanke shawarwari masu inganci don al’ummar duniya da muke yi wa aiki, tare da samar da ƙwarewa mai ma’ana ga kowa. Meta na ganowa tare da gudanar da tsare-tsare da za su taimaka wajen ɗaukar ma’aikata, ci gaba tare da riƙe gungun ƙwararrun ma’aikata daga sassa daban-daban.



## Rungumar bambance-bambance, da adalci da tafiya da kowa na nufin muna:

- Yi ƙoƙarin wajen tabbatar da adalci da kuma daidaito ga damarmaki a wajen ɗaukar aiki, ƙarin matsayi, tare da ƙwarewa ta kashin kai dangane da takardu da ƙwarewa
- Ana girmama bambance-bamance tsakanin mutane da kuma yanayinsu kuma ba a yarda da nuna bambanci ko tsangwama a kowane irin dalili na kowace **halayya mai kariyar doka**
- Ana maraba da hikimomi, ra’ayoyi, da hanyoyin tunani da suka bambanta da namu (da ake kira bambancin zurfin tunani) sannan da haramta miyagun ɗabi’u, waɗanda suka haɗa da kyara, cin zali da tada hankali a wurin aiki, cin zarafi, nuna bambanci da ware ɗaiɗaiku da ƙungiyoyin da suka bambanta
- A samar da wurin aiki da ake girmama kowa ta hanyar tantance abubuwan da muke so da waɗanda ba mu so da cire duk wani shinge da ke hana a tafiya da kowa, mayar da hankali ga daidaito tsakanin mutanenmu da kuma hanyoyin gudanar da kamfani domin a samu adalci da daidaito, kasancewa abokin dogaro da kuma tsayawa wasu.
- A sanya kuɗi ga jin daɗi da walawalar ma’aikatanmu ta zahiri, da ta baɗin ta samar da ilimi mai gudana a cikin tsari na tafiya da kowa ga al’umma mabambanta

Ƙarin jagoranci:

- **Dokar Tabbatar Da Daidaito a Wajen Ɗaukar Aiki**
- **Bambance-bambance da Adalci da Tafiya da Kowa**
- **Dokar Nuna Tsangwama**



## Bambanci a Meta

Meta na ƙoƙarin gina wurin aiki da ake damawa da kowa inda dukkan Ma'aikatan Meta za su san ana yi da su tare da girmama su da duk wani sauyin da suka kawo. Meta Ya haramta nuna bambanci a kan:

- Jinsi ko launin fata ko ƙabila ko asalin ƙasa
- Shekaru
- Addini ko aƙidar addini (ko imani)
- Jinsi, har da masu ciki, haihuwa, shayar da mama, shawarwari kiwon lafiyar ma'aurata ko wasu sharuɗɗa likitoci
- Ɗabi'ar jima'i
- Jinsi, shaidar jinsi, alamomin jinsi, yanayi na shu'umcin jinsi ko daidaiton jinsi
- Ƙasa, matsayin shige da fice, zama ɗan ƙasa ko gadon kaka da kakanni
- Matsayin aure
- Matsayin kariyar soja ko tsohon soja
- Nakasa ta jiki ko ta ƙwaƙwaluwa, yanayin lafiya, bayanan gado ko rabe-rabe (ko waɗanda suke ga mamba na iyali)
- Ra'ayoyin siyasa ko aiki
- Matsayin wanda aka ci zarafi ta bugu, cin zarafi ta lalata ko tsana
- Duk wani abu da aka haramta a ƙarƙashi dokar da ta dace

## Dabarun Meta na bambanci da daidaito da damawa da kowa

### Nemo

Don taimaka mana mu gina tawaga da ke da masaniya a kan bambance-bambance, muna ɗaukar hayar ƙwararrun mutane a fannonin rayuwa mabambanta. Wannan zai taimaka mana wajen amfana da ƙwarewar juna da tunani mai kyau tare da samar da kayayyaki da ayyuka da aka tsara domin kowa da kowa.

### Girma da ɗorewa

Daga kan ɗauka zuwa kula da ƙwazo don samar da tsare-tsare ilimantar da al'umma, muna bayar da taimako da kayayyaki don taimaka jama'a su habaka—a sana'ance da kuma na kai. Muna taimakon mutanen da ke aiki a nan don su faɗaɗa zubin ƙwarewar su—da ya haɗa da iyawarsu don samar da muhallanni ƙungiya inda za a gani, ji a kuma girmama kowa. Meta, da masana'antun fasaha, dole su kasance wani sararin da ake maraba da kowa sannan kowa yana da damar samun nasara.

### Mutunci

Don samar da kayayyaki da samar da manufofi, tare da hidimta wa jama'a da kyau a duniyarmu ta bai ɗaya, dole ne mu yi amfani da tunani mabambanta a dukkan abubuwan da muke yi. Muna amfani bambancin jama'ar ke aiki a Meta don samar da dabaru a kayayyaki da manufofi da tsare-tsare da aikace-aikace sannan mu aiwatar da waɗannan abubuwan da aka koya don samarwa ga kowa.

# Kasance mai kirki da girmamawa

## Alhakinmu ne mu samar da ingantacciyar al'umma mai aiki da kowa, wadda ta ke gudana da ƙwarewar da mutane suka samu ta yin aiki a Meta a kowace rana.

Yana da matuƙar muhimmanci cewa Ma'aikatan Facebook su ji suna da daraja da martaba kuma a yi mu'amala da su cikin adalci a wurin aiki da wuraren da suka danganci aiki, a ƙashin-kai ko bai-ɗaya. Yaɗawa, bayar da amsa, yin muhawara da yin tambaya, duk cikin mutuntawa, da girmamawa muhimman abubuwa ne daga ɗabi'unmu sannan kuma babban makami ne ga manufarmu.

Wannan ɗabi'ar ta taimaka wajen dasa gaskiya da amana da muke buƙata da yanke muhimman shawarwari tare da samun tasiri mai kyau a duniya. Meta bai yarda da tsangwama, nuna bambanci, barazana, takurawa ko kuma kowace irin makamanciyar ɗabi'a ga kowane mutum ba.



## Kasancewa masu kyautayi da girmamawa na nufin muna:

- Mu'amala da kowa a cikin al'ummar da girmamawa, ba tare da la'akari da matsayi, muƙami, girman matsayi, matsayin aiki ko tsawon lokacin aiki ba
- Kula da buƙatu da tunanin wasu da kuma yadda za a fahimci kalamai da matakanmu
- Kada ka yi barazana, ko tada fitina ko cin zalin wasu, har ma da na lalata
- Kada ka zagi, takura, ƙasƙantar, kunyatar ko tozartar da wasu kuma ka kasance mai lura da alamomin da ke nuna cewa an tsangwami ko takurawa wasu
- Kada ka yi ramuwar gayya a kan wasu— ya kamata kowa ya nuna kyawawan ɗabi'u inda kowa zai iya kai ƙorafin wata damuwa ba tare da tsoro ba
- Yi magana game da duka wani abu da zai iya saɓa wa manufofin muhallin aiki masu ƙima na Meta (ka tuna, ana buƙatar manajoji su kai rahoton ainihin Saɓawa ko yiwuwar saɓawa Dokar Nuna Tsangwama, a ƙa'ida cikin sa'o'i 24)

Ƙarin jagoranci:

- **Dokar Nuna Tsangwama**
- **Dokar Kwarmato da Ƙorafi ta Meta**
- **Abin da ake tsammani na Tafiya tare da Al'umma**

## Me ake nufi da tsangwama?

Tsangwama wata ɗabi'a ce, da take ɗamfare da wata **halayya mai kariya**, wadda ke haifar da rashin girmamawa da tsoratarwa da ƙiyayya da ƙasƙantarwa da tozartawa ko muhallin cin zarafi. Ba za a taɓa yarda da ita ba a Meta. Ka tuna: tsangwama ta shafi tasirin—yadda wasu ke kallon wani mataki, ba niyya ba. Alal misali, za ta iya zama:

- **Abin da mutum yakan faɗa ko yakan rubuta**, da suka haɗa da ɓatanci ko zolaya ko yin mummunan zato da kuma barazana, ɗaga murya ko kakkausan harshe ko ɗabi'a, bisa **halaye masu kariya** kamar jinsi launin fata, ɗabi'ar jima'i ko jinsin halitta
- **Abin da wani mutum yakan yi**, kamar shafar da ba a so, yin abubuwan da ke tayar da sha'awa, tare hanyar wucewar wani, ƙin kulawa da wani ko tozarta wani da gangan
- **Abun da wani mutum yake nunawa**, kamar nuna hotuna liwaɗi ko kalaman ɓatanci a wurin aiki ko rarraba su ta kwamfuta. Wannan ya haɗa da rarraba saƙonnin nuna bambanci game da wani tare da wani daban.

**T:**
Sabon manajana mai sauƙin kai ne mai ƙwaƙƙwa. Za su yi tunanin cewa yana da sakin fuska, amma yana ƙwaƙwance tambayoyi game da rayuwa ta kai wanda haka ya hana ni samun sukuni. A hirarmu ta farko 1:1 sun tambaye ni ko na yi aure da 'ya'ya. Na ɗauka cewa suna son su ƙara fahimta ta da kyau tare da ƙarfafa alaƙarmu, amma a al'adata, ba a cika takalo tattaunawa game da rayuwar kai da kai tare da abokan aiki ba. Na kauce wa tambayarsu, amma kuma a wata tawagar aun ƙara yi mini irin wannan tambaya a gaban wani gungu. Na ba da amsa da cewa ba na son tattaunawa abun da ya shafi rayuwata a wurin aiki. Sai suka ce, "Idan nagartacciya ce, ba za ki dace da wannnan tawagar ba. Kina cikin Amurka ne a yanzu kuma muna son mu fahimce ki ne da kyau." Na faɗa wa tawagar game da asalin iyalaina amma sun ji kunyar martanin da manajana ya yi. Me zan iya yi?

**A:**
**Yayin da wataƙila manajanka yana da kyakkyawar niya, bai kamata ka kasa samun sukuni ko tozarta ba, musamman bayan ka bayyana cewa ba ka son tattauna abubuwan da suka shafi rayuwarka. Babu gurbin wannan a Meta. Muna mayar da hankali kan tasirin jawabi ko mataki fiye da niyya. Ka tuntuɓi wani manajan ko ɓangaren shari'a ko Abokin hulɗar Kasuwanci na HR ko Abokin Hulɗa na Dangantakar Ma'aikata, ko ka tuntuɓi SpeakUp, don cigaba da tattauna matsalarka. Kowane daga cikin waɗannan zaɓuka za su ba mu damar taimakawa a magance matsalar. Za a kare ka daga duk wata ramuwar gayya.**

# Ka samar da muhallin aiki mai tsaro

## A duk inda muke aiki, muna sane da tsaronmu da ayyuka na kiyaye lafiyarmu domin mu da waɗanda muke tare mu ci gaba da rayuwa.

Ko dai kana aikin ofis ne, zirga-zirga zuwa ko tafiya wurin aiki, a gida, a ɗakunan gwaje-gwaje, a cibiyoyin bayanai ko wajen duniya, ba abin da ke da matuƙar muhimmanci kamar zama cikin tsaro da ƙashin lafiya. Muna kula da walawalar juna, muna son ƙirƙirar halayen da a cikinsu muka tsira daga cutarwa da kuma 'yancin gudanar da mafi kyan aikinmu.



## Samar da muhallin aiki mai tsaro na nufin mu:

- Bi ƙa'idoji da jagorori da dokoki da suka dace na muhalli, kiwon lafiya da tsaro
- Kare muhalli da al'ummar da muke gudanar da kasuwanci a ciki
- Kada ka yi aiki a lokacin da cikin tasirin haramtattun ƙwayoyi, kayan shaye-shaye, ko kuma duk wani abun maye da zai yi tasiri a tsaro da aiki
- Kada ka ji an takura ka ko ka takura wasu su sha giya a wajen sha'anin aiki ko tare da abokin aiki; idan kana sha giya a wajen sha'anin aiki, to ka yi hakan cikin mutunci
- Ka yi biyayyaka ga dokokin kamfani da suka danganci yin tafiya ka kuma yi amfani da tsarin kula da tafiye-tafiyen kamfani (misali CWT)
- Ka yi kyakkyawan hukunci da kai rahoto a kan kari game da halayyar ma'aikaci ko mai ziyara da za ta iya zama alamar barazana ko tashin hankali
- Yi biyayya ga dokokin Kamfani da suka shafi tsaro na zahiri, da suka haɗa da baƙi, samun damar shiga gine-gine da kuma amfani da bajen Ma'aikatan Meta

Karin jagoranci:

- **Dokokin Baƙi**
- **Dokar Tsaftar Muhalli da Tsaro**
- **Dokar Kawar da Ƙwayoyi daga Wurin Aiki**
- **Dokar Kula da Tashin Hankali a Wurin Aiki**
- **Wiki na Tsaftar Muhalli da Kiwon lafiya da Tsaro na Duniya**
- **Tallafin Tafiye-tafiye a Duniya**

**T:**
Wata tawaga ta abokan hulɗata daga waje za su zo su ziyarci ginin ofishina. Abokan hulɗata sun nemi ko za su iya ɗaukar hotuna da bidiyo a lokacin da suke zagayawa a muhalli. Haka kuma, a lokacin da nake raka su cikin muhalli, na riƙe ma wani ƙofa ba tare da baji ba wanda ba ya daga cikin tawagata. Ko an yarda da irin wannan?

**A:**
**Baƙi suna iya ɗaukar hotuna da bidiyo a waje, a cikin shagon shayi, a zauruka, a wuraren da aka tanada don ɗaukar hotuna (kamar ɗan ƙaramin ɗaki) da kuma gaban Bangon Facebook, inda ba a ganin bayanan sirri da aka bayar. Baƙi ba su da hurumin ɗaukar hotuna da bidiyo a wuraren ayyukan Meta, a ɗakunan taro, ko kusa da kwamfuta ko farin allon bango.**

**Haka kuma baƙi za su iya ɗaukar hoton bajen ƙofa ko kyamarorin tsaro. Ba mu son a yaɗa bayanan sirri a waje ko a wallafa a bainar jama'a ba tare da izini ko saninmu ba. A keɓance, yayin gayyatar baƙi zuwa ofisoshin Meta, ka raka baƙinka kawai da suka yi rajista—yayin da zai iya zama kyautatawa ka buɗe ƙofa ga wasu, wannan ɗabi'a da tana jawo matsalolin tsaro da kariya. Kai rahoton masu ziyarada babu mai rakiya ga Tsaro na Duniya.**

**T:**
Na damu game da abokin aikina. Na san shi da fara'a, abun dogaro kuma jajitaccen a wurin aiki. 'Haka kuma, ya sauya, a 'yan watanni da suka shuɗe, ya keɓe kansa, marar aiki da ƙiyayya a wasu lokuta kuma ya kan saba wasu muhimman wa'adin kammala aiki. Ta yaya zan tabbatar lafiyarsa ƙalau a lokacin da nake lura da tawagar?

**A:**
**Mun damu da mutanenmu da walwalar su ta jiki da ta ƙwaƙwalwa. Ya kamata a tafiyar da yanayi irin wannan da matuƙar taka-tsantsam, sannan ya kamata ka haɗu da Abokin Hulɗar Kasuwancin HR ko Abokin Hulɗa na Dangantakar Ma'aikata kafin ɗaukar kowane mataki. Idan kana tsoron zai iya kawo barazana ga kansa ko ga wasu, ya makata ka tuntuɓi GSOC da gaggawa (ta hanyar tsaro@ ko Taɗin Kai tsaye ko lambar wayar da ke jikin bajen ka).**



# Zama mai biyayya da gaskiya

## Muna kauce wa saɓanin muradu don yin zaɓuka masu kyau ga Meta, waɗanda ba su cuɗanya da muradun kai ko dangantaka ba.

Dukkanmu muna da muradun ƙashin kai da suka sa muka bambanta kuma suke ba mu damar kawo cigaba ga Meta. Duk da haka, mukan fifita Meta a duk lokacin da muka zo aiki ko muke wakiltar Meta. Dole Koyaushe mu riƙa amfani da kyakkyawan hukunci kuma mu nisanci yanayin da zai sa muradun ƙashin kanmu da dangantaka su ci karo da kyawawan muradun Meta, kamar kasuwanci na ƙashin kai ko sayen hannun jarin abikin hamayya.

**Lura:** Hukumar Daraktoci ta Meta za su riƙa samar da wasu dokoki daga lokaci zuwa lokaci idangane da cin karon muradu na daraktoci don su magance wata matsala da ta taso daga ayyukansu a matsayinsu na mambobin hukumar. Duk wata doka za ta shafe cin karon muradu na sama matuƙar yadda za a iya aiwatar da ita.

Karin jagoranci:

- Dokar Saɓanin Ra'ayi
- Cin Karon Muradu na Wiki
- Kayan Aikin Cin Karo Muradu



## Zama mai biyayya da gaskiya na nufin mu:

- Za mu tabbatar cewa kasuwancin Meta yana da faɗi sannan yana sauyawa akai-akai, wanda hakan yana nufin abin da ya cancanta a matsayin ingantattun muradun saɓani da kuma samun canje-canje.
- A kauce wa jawo cin karon muradu da ya ta'allaƙa a kanka. Idan ana maganar wasu ayyuka na waje, ka yi bitar jagoran da ke hannu game da bambanci da ke zuwa, ka tattauna irin yanayin da manajanka sannan ka gabatar da buƙatar neman bitar saɓanin ra'ayi ta hanyar kaya aikin saɓanin. Kafin ka fara kowace daga cikin waɗannan damarmaki, sami izini ta hanyar amfani da kafar yanar gizo ta saɓanin ra'ayi.
- Kada ka bar duk wata alaƙa ta ƙashin kanka ko ta iyalanka su sami wani amfani daga matsayinka a Meta ko su yi tasirin da bai dace ba ko bayyanar tasirin da bai dace ba, a zartas da hukuncinka.
- Ka yi matuƙar ƙokarinka a wurin aiki a kowace rana, kada ka bar ayyukan waje sun hana ka ba da gudummawa ga kasuwanci.
- Ka lura cewa bai kamata a yi amfani da damarmakin kasuwanci da aka gano ta amfani da dukiyar Meta ko bayanai ko matsayinka don buƙatar kai ba.
- Zaƙewa wajen gano yanayin da zai iya jefa muradun Meta su iya cin karo da naka.
- Gaggauta bayyana tabbataccen cin karon muradu, wanda ake ganin yiyuwarsa ko wanda ake zato ta hanyar kafar intanet.
- Guji shiga wani aiki na waje da buƙatar sake dubawa yayin da ake tantance buƙatar.
- Ka sani cewa kayayyaki da ma'aikatan wucin gadi za si iya samun haanyoyi mabambanta da abubuwan da ake bukata game da cin karon muradu; ka tattauna da manajanka ko manajan awonka, don CWs idan akwai wata damuwa.

## Ko ina da wani cin karon muradu?

Cin karon muradu na iya faruwa yayin da mu, ko a wasu lokuta 'yan uwanmu makusanta na gida, suna da dangantakar, kasuwanci ko ta kuɗi dangantaka ta kusa da tamu ta yanzu ko ta baya ko mai yiwuwa:

- **Abokan ciniki da masu kawo kaya**
- **Masu kula**
- **Abokan hamayya da sauran wasu na daban**
- **Masu amfana da kyauta ko tallafin kamfani**
- **Ma'aikatan Meta**

Ga wasu misalai na yanayin da tabbataccen cin karon muradu, yiyuwar sa ko wanda aka zaci faruwarsa da za su iya tasowa wanda kum dole a bayyana su:

- Kai tsaye ko ta shamaki yana kula da wani daga iyalinsa, aboki makusanci ko abokin hulɗa makusanci a Meta ko a inda wani mai samar da kaya ga Meta ya ɗauke su aiki
- Ɗaukar haya ko ayyukan wuraren kasuwanci mallakar ko wanda ke karkashin Ma'aikatan Meta
- Dangantakar da ba ta aiki ko ta kasuwanci ko ta shawara ko ta ba da shawara ba, da wani kamfani
- Shiga harkokin koyarwa ko bincike
- Rike wani mukami na siya ko yin takarar wani mukami na zaɓe
- Sa hannun jari fiye da 2% na jimillar hannun jarin kamfanin da ke kasuwanci a bayyane
- Sa hannun jari a kamfanoni masu zaman kansu waɗanda suke abokan hamayyar Meta ne a yanzu ko nan gaba ko kuma suna da wata alakar kasuwanci da Meta
- Yin aiki a matsayin mai ba da shawara ga kamfanoni masu kula da asusun hannun jari ko ba da shawara kan ayyukan asusun hannun jari
- Yin aiki a matsayin wani mamba na hukuma ko darakta ko humar ba da shawara ta wata ƙungiya ta waje, wadda ba ta neman kuɗi ba ce




## Na damu cewa wataƙila ina da wani cin karon muradu—meya kamata na yi?

1 Ka tattauna bambanci ra'ayinka da za a iya samu da manajanka ko ka tambayi tawagar Ɗabbaƙawa da Ɗa'a don samun jagoranci.

2 Idan kana ganin muradi na ƙashin kai ko aiki, zai iya tasiri ko yake da alamun yin tasiri, da muradun Meta, akwai buƙatar ka cike kuma ka miƙa buƙatar sake yin bitar cin karon muradu ta hanyar **kayan aikin saɓanin**—ka tabbata ka bayar da dukkan bayanan da ake buƙata.

3 Manajanka ko kuma tawagar Saɓanin Ra'ayi zai yi bitar buƙatarka sannan ya bibiyi lamarin zuwa mataki na gaba. Manne wa kowane irin jagoranci da manajanka da tawagar cin karon muradu suka samar.

4 Idan an amince da aiki a waje kuma ake buƙatar yarjejeniya a rubuce, wataƙila a buƙaci Kari na Yarjejeniyar Ayyuka.

# Kare bayanan sirri na Meta

## Ba ma amfani ko bayyana bayanan sirri ta hanyar da ba ta dace ba.

Bayyanawa (ko "tona") bayanan sirri a wajen Meta ko ga waɗanda ba sa buƙatar sa don dalilin halastaccen kasuwanci zai iya haifar da mummunan sakamako ga kasuwancin Meta kuma zai iya zama an karya doka. Alal misali, tonawa za ta iya jawo wa Meta ɗaukar nauyi ko bayar da dabarun samar da kaya ga abokanan hamayya; kuma za su iya jawo shigar da ƙara a kotu ko zagon ƙasa ga aikin, ko kariya, ta abokan aikinmu. Yaɗa bayanan sirri na Meta ga mutane na ciki ko na waje, waɗanda ba su da halastacciyar buƙatar su san wannan bayanin zai iya yin mummunar illa ga mutuncin Meta tare da cin amanar wasu, da suka haɗa da mutanen da ke amfani da ayyukan Meta da abokanan aikinmu da wasu na daban da kuma al'umma.

## Kare bayanan Meta na sirri yana nufin:

- Ka fahimci yadda Meta ke bayyanawa da kuma **rarrabe bayanan** sirri a manufofin Kamfani
- Kada ka miƙa ko ka bayyana ko kuma ka aika bayanan sirri ko na kafawa ko na gasa ko wasu muhimman bayanai na Meta ko wani can daban zuwa wajen tsarin Meta (misali zuwa ga wani can daban ko rumbun adana bayananka ko na'urarka ko asusu ko Tsarin Rubutun Babban Harshe na wani can daban) sai dai idan akwai izini na musamman daga ɓangaren shari' ko XFN ɗinka na sirri
- Kada ka rarraba bayanan sirri a cikin gida sai dai kawai ga waɗanda ke buƙatar su saboda aikinsu
- Yi biyayya ga sharuɗɗan NDA ko yarjejeniyoyin da ke aiki yayin mu'amala da bayanan sirri na wani daban, da ya haɗa da samun rubutaccen izini idan aka nemi ka yaɗa bayanan sirri na wani daban ga wani mutum na daban
- Kada ka kawo ko yaɗa duk wasu bayanan mallaka na sirri na wani tsohuwar ma'aikata ko wuri ga Meta
- Kada ka tafi tare da wani bayanin sirri na Meta idan ka bar aiki da Meta, kuma ka mayar da shi idan nan take idan da ka yi.
- Ka cire mutanen da ba sa aiki da kamfani a yanzu daga sadarwa da bayanai da kayan aikin da suka danganci aiki
- Ka tuna ka aika da neman 'yan jaridu game da dukkan batutuwan da suka danganci kasuwancin Meta wanda za ka yi magana a kai zuwa ga **Press@** Bai kamata ka yi mu'amala da 'yan jaridu ba a madadin ko ka ba da shawara ko bisa zato ka yi magana a matsayin wakilin Meta. Dokar ba ta kuma ba ta nufin hana mambobin al'ummarmu da yin mu'amala da 'yan jaridu a ayyukan da suka shafi kariya ko duk wani ma'aikaci don tattauna albashi ko alfanu ko sharuɗɗa da dokokin aiki a Amurka.
- Ka fahimci nauyin da ke kanka a ƙarƙashin yarjejeniya ɗaukanka aiki
- Kada ka samar da wani sauti ko ka naɗa a na'uraba tare da izini ba

Karin jagoranci:

- **Dokar Ayyuka Na Waje**
- **Bayanan Jagora na Sarrafa Bayanai**
- **Dokar Sadarwar Na'ura**
- **Tsayayyen tsarin Rabe-raben Bayanai**
- **Tsayayyen tsarin Yaɗa Bayanai**
- **Dokar Naɗar Sauti ta Duniya**

## Waɗanne ne misalai na bayanan sirri?

A ƙasa ga wasu misalan bayanan sirri a Meta. Idan ba ka da tabbacin ko za a ɗauki wani abu a matsayin bayanin sirri, ka ɗauka kawai bayanin sirrin ne, sannan ka tambayi sashen Dokoki don ƙarin haske ko ka tuntuɓi Yarjejeniyarka ta Bayanan Sirri da Ƙirƙira (CIIAA) ko Yarjejeniyar Sirrantawa don ƙarin haske.


- Bayanan mallaki
- Kasuwanci a ɓoye
- Tsare-tsaren kayayyaki
- Sabuwar dabara
- Littafan rubutu na ɗakin gwaje-gwaje
- Hanyoyi
- Tsarawa
- Zane-zane
- Bayanan fasaha ko na aikin injiniya
- Bayanan Mai Anfani Na Meta
- Jerin Sunayen Kwastomomi ko Masu Kawo Kaya
- Bayanan Ma’aikan Meta (waɗanda ba na ka ba ko waɗanda aka ba ka izinin yaɗawa ba)
- Makwafai
- Hadwaya
- Bayana kuɗi
- Kasafin kuɗi
- Farashi
- Tsare-tsaren kasuwanci ko wasu bayanan kasuwanci
- Tattaunawa ta cikin gida game da shawara a kan kumshiya
- Shaidar ma’aikata na musamman ko ma’aikatan wucin gadi waɗanda ke cikin ayyukan bitar ƙumshiya

**T:**
Ni manajan sayarwa ne na Meta. Wani abokin harka kasuwancin kan intanet yana bibiya bayan ganawar gabatarwa. Wani dai zai iya zama abokin ciniki yana neman na samar da bayanan da zai gamsar da shugabansa ya ƙara kashe kuɗin talla kamar bayanai daga wani abokin cinikinmu da suke nuna yadda wannan abokin ciniki ya sami nasara ta hanyar ƙara kashe kuɗin tallansu> Wannan zai iya zama wata gagarumar nasara ga tawagata, don haka na ke ganin ba wata matsala na samar da bayanan.

**A:**
**Faɗaɗa kasuwancin Facebook da dangantaka na da matuƙar muhimmanci. Sai dai kuma, akwai buƙatar mu tuna da muhimmancin kare bayanan sirri. A wannan lamari, bayanan sirri game da Meta da sauran ‘abokan harkar kasuwancin kan intanet suna iya kasancewa cikin haɗari idan aka yaɗa su. Ba tare da takamaimen izini da wata yarjejeniyar rashin bayyana sirri ba, ba za a iya yaɗa wata bayanan da ba a bainar jama’a suke ba.**

## Tonawa na cutar da mu baki ɗaya.

Ko da niyya ko babu niyya, tona bayanai na sirri yana illata damar Kamfani ta ya raba bayanai cikin sirri a cikin gida, wanda yake wani ɓangare muhimmi na al'adar Meta kuma muhimmi ga nasara ta Kamfani.



Lura: Wata "tonawa" ba ta haɗawa da sadarwa kai tsaye tare da ko samar da takardu ga hukumar gwamnati game da yiyuwar saɓa wata doka, koda ba a bayyana ga Meta ba. Duk wanda ya ke kai wannan koken za a kare shi daga ramuwar gayya.

**Kada ka yaɗa bayanan sirri na cikin gida a wajey ko a cikin gida ba ga mutanen da aikinsu yake buƙatar sa ba. Ga Misali:**

- Bayanani sirri da/ko bayanan mallaki da aka rarraba a cikin gida a Q&As, Aike-aikena Wurin aiki da Kowa da Kowa.
- Ɗaukar hotunan allo na sababbin kayayyaki
- Dabaru game da ƙaddamarwa ko sigogin da ba saki ba ga abokai, iyali, marubutan bulog ko tsofaffin Ma'aikatan Meta
- Ayyukan kuɗi da sakamako
- Yiyuwar haɗewa wuri ɗaya, samu ko ƙulla hulɗa

Miƙa tambayoyin 'yan jaridu ga **Press@**

**Yaɗa bayanan sirri bisa kuskure ko ba zato shi ma an ɗauke shi a matsayin tonawa.**
Dokarmu ta cikin gida ta "ƙudurci kyakkyawar niyya" ba ta aiki a nan. Har yanzu ya saɓawa nauyin da ke kanmu ga Meta yayin da wani ya yaɗa bayanan sirri a waje ko a cikin gida ba ga waɗanda musamman suke da buƙatar sani, ko da kuwa an yi shi ne bisa haɗari ko da kyakkyawar niyya.

Ba tare da la'akari da niyya ba, ana ɗaukar duk wani fitar da bayanan sirri da matuƙar muhimmanci.

**Ka kula da kewayenka.**
Bajen ka ko abun mannewa ko kuma sabuwar sitikar kwamfutarka za su iya bayyana cewa kana yi wa Meta aiki, musamman a kusa da ofisoshinmu. Ka kula da kewayenka a lokacin da ka ke aiki a wajen ofis ko a gida don hana fitar bayanai na sirri ba zato.

- Kada ka riƙa tattauna maganganun sirri a wuraren zaman jama'a.
- Idan kana son yin aiki a tsarin zaman jama'a—ala misali, a kan jirgin sama ko na ƙasa, a tasha, ko a shagunan shan gahawag—ka riƙa amfani da madubin fuskar kwamfuta na daban.
- Ka kula a duk lokacin da kake aiki a gida kada ka bayyana muhimmin bayani ko bayanin sirri a gaban wani.

Dole ne mu yi taka tsantsan, a duk lokacin da muke a muhallanmu. Wataƙila baƙi da abokan aiki za su iya kasancewa a wuri su ji ko su ga abubuwan da ya kamata a sirranta.

# Kare kadarorin Meta

## Muna yin amfani tare da kare kadarori da kayayyakin Meta, don mu iya samar da cikakkiyar moriya ga duniya.

Dole mu duka mu zama masu gudanar da kadarorin Meta, ko dai na zahiri, bayanai, na kuɗi, na fasaha ko na ilimi. Nasarorin Meta suna cigaba da samuwa a tare da buɗaɗɗiyar ƙirƙira, haɗin guiwa da gano sababbin abubuwa. Damar Meta wajen saurin haɓaka da ƙirƙira sun ta'allaƙa ne ga kare kadarori, bayanai da hikimomin da ke kawo mana cigaba.



## Kare kadarorin Meta yana nufin mu:

- Ka bi jagoran aiwatarwada aka samar, ta la'akari da nau'in kadara da dabarun kasuwanci, don kare fasahar ilimi ta Meta (IP) da dukkan bayanan sirri
- Ka mutunta haƙƙokin IP da na bayanan sirri na kowa, haɗi da na wasu can daban da Ma'aikatan Meta da abokan hamayya, da masu amfani
- Yi amfani da kadarorin Meta da kayayyaki cikin kulawa a halastattun manufofin kasuwanci—kada a sace, lalatawa ko amfani da kadarori don muriyar ƙashin kai
- Kula da shirin kanikancin zamantakewa
- Bi dokokin da jagoran aiwatarwa na Meta yayin amfani da kadarori da kayayyakin Meta dan amfanin na ƙashin kai
- A kula da tsaron kayayyaki fasaha da Meta ya samar da kuma na'urorin ta ƙashin kai da aka yi amfani da su a kasuwancin Meta
- Yi biyayya ga dukkan dokokin da ke aiki, matakan kulawa da manufofin Meta da suka shafi ajiye bayanai da riƙe bayanai.
- A kai rahoton duk wata alama ta damfara ko lalatawa wadda ta shafi kadarorin Meta

Ƙarin jagoranci:

- Dokar Kare Bayanai
- Dokar Aminta da Yin Amfani
- Bayanan Jagora na Sarrafa Bayanai
- Dokar Kula da Odar Rajista ta FTC
- Dokar Tsarin Cigaba da Amfani da Odar Rajista
- Kare Kadarar Meta ta Sirri

**T:**
Yanzu na fara aiki a Meta. A wurin aikina na baya, Ina aiki ne a kan wani shiri mai buɗaɗɗen bayani kuma zan so in cigaba da haka. Me ya kamata in sani game da matsayar Meta a kan IP da ƙirƙira mai buɗaɗɗen bayani?

**A:**
**Meta yana kashe kuɗi matuƙa a dukkan ɓangarorin bunƙasa IP don samun damar cigaba da nasararmu, a matsayin mai ƙirƙira da kuma a matsayin mai ba da gudummawa ga al'ummar duniya. Meta na cigaba da ƙirƙira a bayyane duk lokacin da aka sami dama (Buɗaɗɗen shiri da wallafe-wallafe, ds.) a matsayin hanyar samar da damar haɗin guiwa a buɗe da gano abubuwa da ƙara bunƙasa yanayin ƙirƙira a duniya tare da samar da daidaiton dama ga fasaha.**

**Shawarar ko a cigaba da ƙirƙira a bayyane ya ta'allaƙa a kan wata dabara ta kasuwanci da nau'in IP, ba a raɗin kan ɗaidaikun ma'aikata ba ne.**

**Domin haɓaka tasirin IP ɗinmu, kowane ma'aikaci yana da rawar da zai taka wajen fahimta da bin jagorancin da aka samar, wanda za a iya samu a shafi Samfura na wiki.**

**T:**
Na shiga cikin jayayya game da tashin ɗaya daga cikintsofaffin ma'aikatana. Mun sha wahala kafin mu gano wasu daga cikin bayanan aikinta. Ban sani ba ko a sasanta jayayyar don haka dai ina adana rajistarta a matsayin ma'aikaciya a cikin wata holda a kwamfutata Ban tabbatar ba ko muna da tsarin jagoran bayanin riƙe bayanai ko kuma ya kamata mu goge wasu ajiyayyun bayanai bayan wani tsawon lokaci. Ba ni da tabbas kan me zan yi?

**A:**
**Sai dai idan ka sami Umarnin Riƙewa, yana da muhimmanci ka bi manufofinmu na riƙewa inda kuma za ka goge ajiyayyun bayanan. Adana bayanai na tsawon lokaci na iya sanya bayanan sirri ko na taka-tsantsam cikin haɗari na buɗewa da kuma amfani da su ta mummunar hanya. Haka kuma mai yiwuwa ne mu sami nauyin shari'a na mu goge bayanai da ba a buƙatar su, kamar bayanin ƙashin kai ko bayanan sirri daga abokin hulɗar kasuwanci. Ida ka ajiye bayanai kamar yadda jadawalanmu suka nuna, kana ƙara ƙarfafa tsarinmu na kula da bayanai da kuma kare Meta. Bi dukkan umarnin riƙewa na doka don ajiye bayanai da suka danganci shari'ar da ke gudana ko wasu nau'ikan jayayya. Idan ba ka da tabbacin abun da za ka yi, sai ka tuntuɓi eDiscovery & Information Governance team (infogov@) don ƙarin haske.**

### Ka sani ne?

Abubuwan da muka gano da tawagar Aiwatar da Bayanai je wajen adana kayayyaki don ci gaba da yin amfani da rajista ko riƙewa don hukuma. Gaba ɗaya, irin wannan nau'in bayanai, daga cikin wasu, za su iya danganta da nauye-nauyen damar yin amfani da rajista tare da riƙewa a dokance:

- Imel da sauran hanyoyin sadarwa ta yanar gizo, har da na Workplace, WhatsApp da sauran manhajojin saƙonni
- Bayanan da aka wallafa a Wiki ko kuma wasu manazarta na gida ko dandalin musayar ilimi
- Dukkan takardun da aka adana a dirayib ko wuraren ajiya na sarari, har ma da Google Docs, SharePoint, OneDrive da Dropbox
- Bayanan da aka adana cikin tsari da ƙaramin tsarin wuraren ajiya, har da Hive

# Mu yi gini cikin mitunci domin waɗanda muke ƙarfafawa

## Ginawa don waɗanda ke amfani da kayayyaki daayyukan Meta yana nufin bai wa mutanewatadamar magana,kare siirida samar da tsaro ga mutane




### A wannan sashen:


Kafa al'adar mutunta bayanai a ɗaukacin Meta 26

Yi gini cikin mutunci 28

A kare dandalin biyan kuɗi 31

# Kafa al'adar mutunta bayanai a ɗaukacin Meta

**Meta ta himmatu wajen kare sirrin mutane Samun al'adar mutunta bayanai yana ba mu damar riƙo da yarda da juna da kuma masu amfani da Meta, kuma ya ba mu damar biyayya ga nauyin doka da ke kanmu.**

Ko muna gina sababbin kayayyaki ne ko ingantawa morewa, ko kuma kula da wani daban, dole ne kowa ya fahimta tare da girmama sirri da wajiban Meta da kuma himmarmu. Mayar da himma ga sirrantawa na nufin ɗaukar alhaki, tsarawa tare sanya sirri a zuci da kuma tabbata cewa mun ci gaba da kare sirri da tsaro na bayanan da aka damƙa mana amana. Za mu cigaba da bunƙasawa da sauyawa da kula da sirri a dukkan ayyukanmu.



## Kafa al'adar mutunta bayanai yana nufin muna:

- Fahimta tare da bin hanyoyi da manufofin sirri na Meta, da suka haɗa da **Dokar Sirrantawa Ta Cikin Gida**
- Muna lura a matsayin kamfani kan hanyoyin da muke tattarawa, amfani, yaɗawa da adana bayanan da suka haɗi da na ma'aikatanmu , na ƙashin-kai na mutane da bayanai a cikin kayayyakinmu da gudanarwa—da yadda muke sarrafawa da kare shi da zarar mun same su
- Yaɗa bayanan da suka zama lalle ne kawai da kuma dacewa da manufar da kuma tabbatar da cewa ba a bayyana bayanan ƙashin kai na taka-tsantsam ba tare da izinin mutumin ba
- Tsarawa tare da sirrantawa a zuci, wanda a wani ɓangare, na nufin bai wa mutane zaɓuka game da bayanan da muka tattara ko muka ƙirƙira game da su, da ya haɗa da samun dama ga da sarrafa bayanansu a duk lokacin da hakan ta samu tare da dacewa da kuma girmama zaɓukan da suka yi
- Ka karɓa, ka ƙirƙira ka samar da dama ka yi amfani da mafi ƙanƙantar bayanan da muke buƙata wajen ƙarfafa dalilan da aka ambata—ba ma aminta da samun bayanai ba bisa ƙa'ida ba
- Ka cike Sake Duba Sirri kamar yadda aka buta kafin ƙaddamar da duk wani kaya da aka gayara ko ayyuka ko wani aiki da yake karɓa ko amfani ko raba Bayanan Mai Amfani ko yin wakilci a waje game da ayyukan sirri da tsaron bayananmu
- Tabbatar hanyarmu ta Sake Duba Sirrantawa da kuma hanyoyin sirrantawa na Kamfaninmu suna tafiya ne tare da Abubuwan da Ake sa Rai Guda Takwas
- Maida martani yadda ya kamata ga sha'anoni da ke yin zagon ƙasa ga sirrantawa, mutunci, ko samuwar bayanan wanda nauyin hakan ke kan Meta
- A riƙa tantance al'adun sirri na Kamfani a kai-a kai don a tabbata muna cimma abin muke fata da na masu ruwa da tsaki da na masu sa ido
- Yi amfani kuma ka shiga kayan aikin intanet da lura da taka-tsantsam, sai dai yadda ya zama wajibi mu yi aikinmu kuma ba don amfanin ƙashin kai ba ko don tallafawa wani mai amfani wajen gujewa ganowa ko hukunci

Karin jagoranci:

**Dokar Sirri Ta Cikin Gida**

**Sirri na Wiki**

**Dokar Damar Amfani da Data ga Mai amfani**

**T:**
Ni ma'aikacin wucin-gadi ne a Meta a matsayin mai sayarwa. Abokina Tom shi ne mai kula da wani shafin Facebook na wata ƙungiyar mawaƙan barbershop. Tom ya tuntuɓe ne saboda an cire ɗaya daga cikin bidiyon waƙoƙinsa, kuma Tom bai san dalili ba. Tom ya ba ni lambobin sirri sannan ya roƙe ni da in shiga a madadin sa don ain gano bakin zaren matsalar sannan in yi amfani da kayan aiki na gida don in dawo masa da ƙumshiyar. Tun da dai bidiyon Tom bai da alƙa da aikina, shin daidai ne in dawo masa da ƙumshiyarsa?

**A:**

**Kada ka yi amfani da bayanan wani don ka shiga cikin asusun sa ko ka yi aiki a asusun wani aboki. Kana shiga bayanan mai amfani da ba su da alaƙa da aikinka. Bugu da ƙari, kana dawo da bayanan da aka cire.**

**Babu laifi ku tattauna game da Meta da abokai, sai dai ba lalle ka iya shiga bayanan mai amfani na mutane ba ko da kuwa na waɗanda ka sani ne. Idan wani aboki ko ɗan'uwa yana samun matsala da asusun Facebook ko Instagram wanda mallakinsu ne, za ka iya miƙa fom ga fburl.com/oops don samun taimako. Meta ba zai taɓa lamunta da shiga bayanan mai amfani da ba ta dace ba, ko da kuwa da kyakkyawar manufa ne.**

**T:**
An sauya ne zuwa sabuwar ƙungiya kwanan nan. Sabon manajana ya aika nema ga IT domin samun izinin ƙarin wata kwamfuta wanda zan yi aiki da iat. Me ya kamata na yi da damar samun izini na matsayina da ƙungiyata da suka gabata?

**A:**
**Ka sanar da IT ko manajanka cewa har yanzu kana da tsohon izini. Kada ka ajiye kwamfutoci ko manhajoji da ba kada buƙata da su a sabon matsayinka. Ajiye su na nuna cewa za ka kalli bayanan sirri da ba kada wata buƙata da su.**

**Kai da manajanka kuna da wani alhaki na ku tattauna samun izinin samun dama da ake da shi a da, da sabo don ku gano abun da ake buƙata.**

**Yana da muhimmanci cewa Ma'aikatan Meta su sami dama ga bayanai da suka zama dole ga gudanar da ayyukan da suke yi a yanzu kaɗai.**



"Samun haƙƙin sirri abu ne mai cigaba da sanya hannun jari na haɗaka a ɗaukacin kamfaninmu kuma nauyi ne a kan kowa a Meta ya bunƙasa manufarmu"

**–MICHEL PROTTI,**
Babban Jami'in Kula da Sirrin Kaya

# Yi gini cikin mutunci

## Meta ta himmatu wajen haɓaka tasirin da muke da shi a kan mutane da al'umma ta dukkan abubuwan da muke samarwa.

Kamar yadda muke ƙara isa ga jama'a kuma muke cigaba da inganta sababbin kayayyaki da tsare-tsare, buƙatar ƙirƙirar kayayyaki masu ƙarin inganci tana ƙara faɗaɗa zama mai sarƙaƙiya. Ƙirƙira kawai ba ta wadatarwa. Ana fatan mu yi ƙirƙira da ta dace da jajircewa wajen hangowa tare da rage tasirin duk wata cuta a dukkan abubuwan da muke samarwa.

## Gini cikin mutunci na nufin muna:

- Ka faɗaɗa tunani a kan yanayi na yiyuwar samun tasiri ga mutane da al'ummomi da jama'a, ta duba mabambantan nauyace-nauyace, kamar tafiya da kowa da kariya da sirri da wasu.
- Ankarar tare da magance illolin da za su iya faruwa da wuri da kuma yawanci a ɗaukacin tsarin samar da kaya ka kuma riƙe haƙƙokin ɗan adam da kyau
- Ka gudanar da nazarin haƙƙokin jama'a daga farawa zuwa aiwatarwa, kamar duba ko al'ummomin da ake dannewa suna da wani ƙwarewa da ta bambanta da dokoki da kayayyaki da al'adarmu
- A nemi shawarar ƙwararru, mabambantan ra'ayoyi da kayayyaki da muke da su a Meta da ke yi mana jagoranci a shawarwarinmu
- Ka shiga cikin ayyukan sake dubawa da lokutan aiki, kamar Sake DUba Sirri da mutuncin XFN da Haƙƙokin Jama'a na lokacin aiki da nauye-nauyen lokacin aiki na AI, ka tattauna kasuwanci da rage haɗari
- Yi aiki da sauri don ganowa tare da cire bayanai masu illa daga dandamalan Meta, kamar kalaman ƙiyayya da cin zarafi, ci da gumin yara, barazanar tashin hankali ko ta'addanci
- Ka tsara ka samar da kayayyakin da suka ba wa tsaro da sirri da mutunci da daidaito muhimmanci a ɗaukacin fasahohinmu
- Ka samar da gargaɗin da ya kamata a inda ya dace tare da bayyana umarni don kariya da kuma amfani da kayayyakinmu yadda ya dace

Ƙarin jagoranci:

- Kyakkyawar Ƙirƙirar Ɗakunan Gwaje-gwajen Zahiri na Meta
- Wiki Na Haƙƙokin Jama'a
- Wiki na Yin Gini Cikin Mutunci
- Wiki Na Haƙƙokin Ɗan'adam

Hanyoyin Ƙirƙira cikin mutunci wasu jeri abubuwa ne da ɗaiɗaikun mutane da al’ummomi da jama’a suke buƙata don yin fafutuka, kuma wanda dandamalan Meta ya kamata su kare. Waɗannan Hanyoyin su ke fitar da ƙa’idoji su kuma samar da wani tsari ga ma’aikatan Meta don yin amfani da hanyoyi wajen ganowa tare da rage tasirin cutarwar da kan iya faruwa a ɗaukacin hanyar samar da kaya.

## HANYOYIN YIN GINI CIKIN MUTUNCI

### Ka ba wa mutane wata damar magana

- Cin gashin kai
- Mu’amala da farar hula
- Magana

### Ka samar da haɗaka da al’umma

- Tattaunawa mai fa’ida
- Walwala

### Yi wa kowa aiki

- Inganta muhalli mai ɗorewa
- Adalci da tafiya da kowa

### Ka sa mutane cikin aminci ka kuma kare sirri

- Sirri da kare data
- Kariya

### Haɓaka damar tattalin arziki

- Tsaron tattalin arziki

## Shin ka sani ne?

**Kariya na ɗaya daga cikin hanyoyin yin gini cikin mutunci.**

Muna da tawaga ta musamman da ke aiki tare da ƙungiyoyi na waje da hukumomin gwamnati don a taimaka wajen bai wa mutane kariya. Misali, akwai rahoto game da zaman kulliya zuwa ga Cibiyar Ƙasa ta Ƙananan Yara da Suka Ɓata da Ci da Gumin Yara don saba ma duk wata doka da ta shafi ci da gumin yara.

Muna da tawaga da aka bai wa horo na musamman don su yi bita, ɗaukaka ƙara da kai rahoton wannan bayanin, wanda dole ne a yi a yanayi na tsaro tare da nuna wa mutane 'yan tsirarru kayan.

Lura: Idan ka ci karo da wannan kaya, kada ka sauke shi, aika shi, ko yaɗa shi.

> "Muna son mu riƙa kirkirar kaya... da hangen tafiya da kowa da daidaito don tabbatar da kayayyakinmu suna kawi ƙima ga kowa."

**–Maxine Williams,**
Babban Jami'in Kula da Bambance-bambance



# A kare dandalin biyan kuɗi

## Za mu taimaka wajen aika kuɗi, shago a duniya, da kuma ba da gudummawa cikin kwanciyar hankali, dole ne mu ba da tamu gudummawa wajen hana miyagun ayyuka.

Mun mayar da hankali wajen samarwa da mutane hanyar biyan kuɗi mai inganci, kuma ɗorarriya. Mun san da cewa miyagun mutane da bata gari suna kai farmaki ga dandalin biyan kuɗi ta yanar gizo, kamar fita da kuɗin haram da tallafa ma 'yan ta'adda da kuɗi. Ana son mu yi biyayya ga tsaren dakatar da kuɗi.

A yayin da muke kula da dandalin biyan kuɗi, doka ta ba mu damar mu sa ido, mu tantance shaidar kwastoma ko mai amfani kuma a kare su ta hanyar kula da ayyukan 'yan damfara da halayen da ake zargi. Muna samar da aiki cikin gaskiya ta sanar da kwastoma da kuma magance kokensa ko ƙararraki cikin lokaci.



## Tsare dandamalin biyan kuɗi na nufin muna:

- Ka fahimci kuma ka bi manufofin Kamfani, hanyoyi da matakan sarrafawa na cikin gida da aka tsara don kange ɓata-gari daga amfani da dandamalan don safarar kuɗin haram da sauran haramtattun ayyuka
- Sa ido ga dukkan ayyukan biyan kuɗi da ake zargi, kamar jinkirin bayar da cikakken bayani ko mahaɗar da ake tuhuma tsakanin masu buga wasa da masu samar da wasa, masu ba da tallafi da ƙungiyar taimakon marayu, ko biya tsakanin mutum-da-mutum, da ɗaga jar tuta da kuma ayyukan da ake tuhuma don Cika umurnin doka da Ɗa'a
- Ɗauki alhakin tantance shaidar kwastoma—wanda ake kira "ka san kwastomominka"—don haka mun san wanda ke amfani da kayayyakin Meta
- Ka kula da sirri a lokacin da ka ke bincike ko kai rahoto ayyukan da ake zargi kuma ka girmama cewa bayanai da suka shafi biyan kuɗi ba lalle ne a yaɗa a faɗin Meta gaba gaɗi ba

Karin jagoranci:


**Wiki na bin dokokin FinTech na Meta**

## Me ake nufi da safarar kuɗi ta haramtacciyar hanya?

Safarar kuɗi ta haramtacciyar hanya yana nufin hadahadar kuɗi ta yadda miyagun mutane, har da miyagun ƙungiyoyi, suke yin ƙoƙarin ɓatar da yadda aka sarrafa da inda aka samo kuɗi, ko nau'ukan haramtattun ayyukansu. Tallafa wa 'yan ta'adda (duk wata gudummawa ta kuɗi ga ƙungiyar ta'addanci, ko na haramtaccen aiki ko ba shi ba) duk ana iya alaƙanta shi da fitar da kuɗin haram ƙasashen waje. Misalan dokokin da ake da su sun haɗa da Bank Secrecy Act (BSA) a Amuruka da kuma Dokar Ireland's Criminal Justice (Fitar da Kuɗin Haram Ƙasashen Waje da Tallafa wa 'Yan ta'adda).

**Ta yaya wannan ke da alaƙa da Meta?**

Muna ba da damar biyan kuɗi tsakanin mutum-zuwa-mutum (P2P), wasu a cikin wasa da sayayyar Marketplace na Facebook da gudunmuwa, kuma muna da walat na kuɗin dijital, waɗanda dukkansu ana lura da su game da safarar da kuɗaɗe.



**Jar tuta ta fitar da kuɗin haram ƙasashen waje**
Dole ne mu sa ido kodayaushe don gano alamomin ayyukan da ake tuhuma ko hadahada. Wasu misalan sun haɗa da:

**Hada hadar kuɗi da ba ta dace da bayanan mai amfani ba**
Wani Mai amfani da ke yin hadahadar kuɗi kaɗan a wata (kuma koyaushe da abokai) kwatsam sai ya biya maƙudan kuɗi ga wani sabon mai amfani na Meta

**Cajin bayanan asusu a kai-a kai**
Kamar suna, bayanan tuntuba ko bayanin biya

**Tsarin ba da sadaka da ba a saba ba**
Sadakar da ta nuna ayyuka masu yawan gaske fiye da yadda aka saba a ba da tallafi ko kuma wani mai ba da tallafi da ke ba da tallafi a kai-a kai a cikin ƙanƙanin lokaci

**Alamomin aikata laifuka a kan dandamalan Meta**
Sayar da ƙwayoyi ko makamai

# Yi gini cikin mutunci tare da abokan hulɗarmu

Kayan fasaha na Meta suna bunƙasa damar tattalin arziƙi da daidaita fagen harkoki. Mu ma, za mu iya yin gini cikin mutunci ne kawai idan muka yi gasa tare da haɗin guiwa mai kyau.



**A wannan sashen:**

| | |
|---|---|
| Bi dokokin kasuwanci na duniya | 34 |
| Yi gasa cikin ƙwazo da adalci | 36 |
| Yi haɗaka cikin mutunci tare da wasu daban | 38 |

# Bi dokokin kasuwanci na duniya

**Da ofisoshi, mutane da kayayyaki a ƙasashe masu yawa a faɗin duniya, Meta ya duƙufa wajen yin biyayya ga dokokin duniya kan fitarwa, shigarwa da kuma sanya takunkumi.**

Muna alfaharin yin hidima ga sama da mutane biliyan uku a ƙasashe da al'adu masu yawa da kuma cikin harsuna masu yawa. Muna ɗaukar hadwaya, softwaya da fasaha zuwa ƙasashe daban-daban. Muna hadahada da kwastomomi, masu kawo kaya, a dunƙule ko ɗaiɗaiku a dukkan faɗin duniya. Wannan na nufin dole ne mu girmama al'adu mabambanta, dokokin kasuwanci da na dakatarwa da gudanarwa a duk inda muke aiki.



## Biyayya ga dokokin kasuwanci naduniyana nufin muna:

- A tantance ɗaiɗaikun mutane, kamfanoni da ƙasashe yadda ya kamata don mu tabbata ba mu saɓa wa wata dokar dakatarwa ba ko shingen kasuwanci
- Yin biyayya ga dukkan dokokin kasuwanci na ƙasa da ƙasa, har da waɗanda suka shafi shige da fice na kayayyaki, ayyuka da tekanika data daga Amuruka zuwa wasu ƙasashe
- Miƙa koke zuwa ga Kotun Kasuwanci idan muna ganin cewa an shigo ko fitar da tekenikal data ko hadwaya ta hanyar da ba ta dace ba
- Ka tuntuɓi Wiki na Kasuwancin Duniya ko ka tuntuɓi tawagar Kula da Dokokin Kasuwanci kafin yin mu'amala da ƙasashe da ɓangarorin da aka sanya wa takunkumi

Karin jagoranci:

- **Dokar Ɗabbakawa ta Kasuwanci na Duniya**
- **Wiki na Dokar Ɗabbakawa ta Kasuwanci na Duniya**
- **Wiki na Tafiya zuwa Ƙasashen da aka sa wa takunkumi**
- **Wiki na International Hand-Carry**
- **TradeLegal@**

## Me ya kamata in sa ido a kai?

Waɗannan ayyuka suna iya kawo sanya takunkumi da/ko haɗarin kasuwanci:

- Haɗin guiwar kasuwanci da kawo kayayyaki
- Fiton kaya na ƙasa da ƙasa da kuma musayar fasaha
- Binciken kasuwa
- Hayar masu yanke shawara
- Biyan kuɗi ga ƙasashen ko ɓangarorin da aka sanyawa takunkumi
- Ƙaurace wa buƙatun da dokar Amurka ba ta ba da izini ba
- Samun kayayyaki da ayyuka



**T:**
Zan yi tafiya zuwa wata ƙasar da ke ƙarƙashin cikakken takunkumi don halarta bukin aure. Tawagata tana aiki kan tsattsauran wa'adi don kammala wani aiki kuma zan so in yi aiki yayin da na ke can. Ko zan iya tahowa da kwamfutar da Meta ya ba ni?

**A:**
**Yayin tafiya zuwa wata ƙasa da take ƙarƙashin cikakken takunkumin kasuwanci na ƙasa da na ƙasa da ƙasa, ana buƙatar izini daga masu Ɗabbaƙawa da Ɗa'a kafin a yi. Wannan ya shafi dukkan wata hadahadar kudi da ta shafi ƙasashen da aka sanyawa takunkumi ko ɓangarorin da aka kange, tare da neman izinin tafiya ƙasar da aka sanyawa takunkumi tare da na'urar kamfani ko wadda yake sarrafawa.**

# Yi gasa cikin ƙwazo da adalci

## Muna yin nasara ne ta yin gogayya da sauran kasuwanci a kan ingancin kayayyakinmu da ayyukanmu.

Gogayya na sa mu ƙara ingantawa da kyau, kamfani ya zama mai ƙirƙira. Dokokin gogayya, ana kiran su da dokokin rashin yarda, don a tabbatar cewa kamfanoni ba su dakatar da gogayya ko kuma su yi amfani da ƙarfin kasuwanci su cutata ma abokanan gogayya.

Biyayya ga dokokin gogayya na taimaka mana wajen kauce ma bincike, saƙara, tara, shinge da kuma ladabtarwa.



## Yin gasa da Adalci na nufin cewa muna:

- Mun yanke shawarar kasuwanci ba tare da kula da abokan gogayyarmu b, ba tare da wata yarjejeniya ko haɗaka da su ba
- Kada ka aminta da abokanan gogayya, kai tsaye, ko kaikaice:
    - Don saita kowane ɓangare na farashi ko wasu sharuɗɗa da suka danganci kayayyaki ko ayyuka da muke samarwa ga wasu
    - Don ba wa kwastomomi, masu talla, iyakoki ko kayayyakin kasuwa
    - Don kauce wa yin mu’amala da wani kamfani na musamman (da ake kira “ƙauracewar rukuni”)
    - A mataki na tayi ko dai a miƙa wani tayi ga kowane irin kasuwanci mai ci
    - Don kauce wa ko dai (i) ɗaukar ma’aikata ko yin hayar (ko wani daban) ma’aikata ko (ii) yin gasa a albashi ko wasu sharuɗɗan ɗaukar aiki
- Kada ka yi musaya ko sadar da wani bayanin sirri ga abokanan gogayya, sai dai idan Kotu ta ba da izini
    - Bayanin sirri na gagayya sun haɗa da bayanan da suke mallaki, na sirri ko ba na jama’a ba kuma suna da alaƙa da ayyukan ɗaiɗaikun kamfani ko dangantaka da masu amfani ko wasu na daban
- Bai kamata ma’aikacin Meta ya yi amfani da bayanan da ba na kowa da kowa ba ko bayanin da kai tsaye ko a kaikaice aka samo daga amfanin masu talla da suke amfani da ayyukan talla na Meta don ya samar da kayayyaki don yin gasa da waɗannan masu tallan, sai dai idan doka ta yarda kafin yin hakan

Karin jagoranci:
Dokar Ɗabbaƙa Hamayya

## Me ya kamata in sa ido a kai?

Misalan da ke ƙasa su iya kawo matsalar shari'a da ke da alaka da gasa a wasu lokuta. A wannan ɓangaren doka inda matsaloli makamanta kan zama masu sarƙaƙiya, nemi shawara daga Ɓangaren Shari'a kafin ka tsunduma cikin ayyuka masu zuwa:

- Tsara wani shiri na musamman wanda Meta zai buƙaci abokin ciniki ya shiga wata yarjejeniya da Meta kuma ban da sauran abokanan hamayya
- Gudanar da cinikin (ko farashi) na wani kaya/aiki na wucin gadi a lokacin da abokin ciniki ke sayen wani kaya/aiki (ana kiran sa da "ɗaurewa")
- Ƙokarin samar da farashin da a kansa mai sake sayar da kayan Meta zai sake sayar da waɗancan kayayyaki
- Dakatar da wata dangantaka da aka fara da ke da muhimmanci ga ɗaya bangaren ba tare da wata ƙwaƙƙwarar hujja ta kasuwanci ba
- Rage kaya ko aikin Meta wanda wasu na daban ya dogara a kai don gudanar da kasuwancinsa, ta yadda abun zai tasiri ƙwarai a gare su idan har ba su samu damar amfani da kaya ko ayyukan Meta ba
- Ɗaukar kowane irin mataki da zai sa wani ya ji kamar cewa Meta ba su yin hamayya cikin adalci ko kuma bai wa Meta fifikon rashin adalci da wasu daban ba su samu ba



# Yi haɗaka cikin mutunci tare da wasu daban

**Muna son mu yi aiki da amintattun mutane na daban waɗanda za su taimaka mana wajen cimma manufofinmu sannan mu yi aiki ta hadin guiwa don mu ƙirƙiro tare da samar da walwala da tattalin arziki.**

Ayyukan Meta tare da dogaro a kan wasu daban, da suka haɗa da masu samar da kaya, da kuma abokan hulɗar kasuwanci, don taimaka mana wajen cimma muradunmu. Za mu iya yin haka ne kaɗai idan mutane na daban ɗin sun cancanta, suna aiki bisa dacewa da kuma martaba, sannan suna biyayya da dokoki, ƙa'idojin kula da manufofin da ke aiki.

Abun da ba zai yiyu ba mai yiyuwa ne idan muka yi aiki da mutum na uku waɗanda suka bayyana bambancin mutane da al'ummar da muke yi wa aiki, waɗanda aƙidunsu da ɗabi'unsu sun yi daidai da namu.



## Yin haɗaka cikin mutunci tare da wasu daban na nufin muna:

- Yi bitar haɗari ga wasu daban sannan ka sami cikakken izini kafin ka fara mu'amala don ka tabbatar su masu sabanin al'adu ne, sun cancanta, kuma sanannu abun dogaro
- Yi ƙokarin yin mu'amala da wasu na daban waɗanda suka dace da manufa da manufar Meta
- Manufar samowa da yin hadin guiwa cikin mutnci ta hanyar neman wasu daban su yi biyayya ga manufofin Meta da saura dokoki da manufofi, kamar sirri da buƙatar tsaro da dokokin hana cin hanci da rashawa da harajin kasuwanci da dokokin sa takunkumi, da kuma **ka'idojin Kawancen Kasuwanci Mai Inganci (RBA)** don gina al'ummomi masu kariya da juriya, mabambanta kuma masu ƙarfin tattalin arziki
- Samowa ta hanyoyin tayi na hamayya da yarjejeniyoyin da aka amince

Ƙarin jagoranci:

- Dokar Kula da MHaɗari na Wasu Daban
- Dokar Samowa da Sayo Kaya Ta Duniya
- Dokar Kwangila
- Ƙa'idojin Sadarwa da Yaɗa Manufa na Waje
- Dokar Sirri Ta Cikin Gida
- Dokar Tsaro ta Wani Can Daban
- Dokar Yaƙi da Cin Hanci
- Ƙa'idojin Bambanci Mai Kawo Kaya

**T:**
Ina cikin aikin nema amincewa (RFP) kuma masu kawo kaya huɗu su ba da amsa. Ɗaya daga cikin huɗun yana da farashi na ƙasa-ƙasa amma bai dace da sauran masu kawo kayan ba ta la'akari da ƙarko. Shin wajibi ne gare ni in zaɓi mai kawa kaya da ke da ƙarancin farashi?

**A:**
**Akwai abubuwa masu muhimmanci da ake lura a lokacin zaɓar mai kawo kaya, farashi na ɗaya daga ciki. A Meta, bayan farashi, akwai da yawan dalilai kan tafi zuwa a shawarar RFP. Waɗannan na iya haɗawa amma ba a iyakance ga ƙarfin mai kawo kaya ba, tsaro, inganci, albarkatu, ƙwarewar fasaha, bambance-bambancen, daidaitawa da tsammanin RBA, shirin ɗabbakawa da ƙaddamar da manufa da darajojin Meta.**



**Ka sani ne?**

Meta ya ƙaddamar da shirinsa na Bambancin yunƙurin Mai Kawo Kaya a Oktoba 2016 don taimaka wa masu kawo kaya su yi kasuwanci da mu da kuma mutane da al'ummomi da Meta ke haɗawa. Manufar shirin ita ce don a sauya yadda mabambantan masu kawo kaya ke haɗuwada abokan ciniki da kuma junansu sannan su samar da kayayyaki don su bunƙasa.

Tun lokacin aka ƙaddamar da shirin, Metaya kashe sama da biliyan $8 a faɗin duniya da kamfanonin aka ba wa shaida a Amurka cewa na marasa rinjaye ne ko na mata ko na tsohon soja ko LGBTQ+ ko na masu naƙasa ne.

Ƙari a kan haɗin guiwar Meta da masu kawo kaya mabambanta, muna tsammanin cewa masu kawo kaya da ke haɗin guiwa da Meta suna yaɗa waɗannan halaye kuma suna samo kayayyaki da ayyuka daga masu kawo kaya mabambanta a inda ya dace.

## Samowa cikin mutunci

A Meta, muna tsammanin masu kawo kaya su:

- Ƙalubalanci tsarin da ake kai sannan ka kawo ƙirƙira ta hanyar inganci,samarwa, aminci da kuma farashi
- Gudanar da ayyuka a wani halin ƙwarewa da yanayin girmamawa sannan ka raba himmarmu ga al'adar ciniki cikin ɗa'a kamr girmama sirri da kauce wa rikici na muradu da cinikin yankan baya
- Maida martani a kan lokaci ga neman bayanai ko bincike
- Tabbatar cewa ma'aikata sun samihoron da ake buƙata na aikin da aka sanya musu

# Yin gini cikin mutunci tare da duniya

Yana da muhimmanci a gina gaskiya a al’umma, gwamnatoci, masu aiwatarwa da al’ummamin karkara, dukkanmu muna da aiki da muke yi. Ta haka ne za mu iya yin gini cikin mutunci yi wa kowa aiki.



**A wannan sashen:**


| | |
|---|---|
| Kasance abin koyi wajen tsare gaskiya a harkar kuɗi | 42 |
| Kada ka shiga a cinikayyar yankan baya | 44 |
| Ka yi sadarwa a bayyane tare da faɗin gaskiya | 46 |
| Ka hana cin hanci da rashawa | 48 |
| Bayarwa da karɓar kyaututtuka da nishaɗantarwa | 51 |
| Ka yi mu’amala da gwamnati da shugabannin siyasa cikin mutuntawa | 53 |
| Samar da duniya mafi nuna kulawa, mai ɗorewa | 55 |

# Kasance abin koyi wajen tsare gaskiya a harkar kuɗi

## Muna ƙirƙira da adana sahihan bayanan kuɗi da na kasuwanci, don mu da wasu a kasuwar mu iya dogaro a kan ingantacce kuma amintaccen bayani game da aikin Meta da tasirinsa.

Sahihai, ingantattu kuma cikakkun bayanai na da matuƙar muhimmanci wajen yanke kyakkyawar shawarar kasuwanci, tare da kare kyakkyawan sunanmu da mutuncin mu’amalolin kuɗi da kuma cimma buƙatunmu a matsayin kamfanin jama’a. Meta, al’ummarmu, masu saka hannun jari, masu gudanarwa da sauransu duk sun dogara a kan bayanan da muke samar musu wajen fahimtar sakamakon hadahadar kuɗinmu sannan su ɗora mu a ma’uni don gwada nasararmu a matsayin kamfani.



## Zama abin koyi wajen tsare gaskiya a hadahadar kuɗi na nufin muna:

- Adanawa, ka adana fayil ɗin ma’amalolin kuɗi da bayanan kasuwanci da kyau, da gaskiya, a kan lokaci tare da bayanan da suka dace, har da wasu takardu da za su taimaka
- Bi dokoki da ƙa’idaoji masu dacewa na lissafi da kai rahoto
- Bi dukkan ƙa’idojin da hanyoyin da Meta ya tanadar na shiga kwangiloli
- Aiwatar da kasafin kuɗi kuma ka riƙe ka sarrafa kayayyakin kuɗi na Kamfani a tsanake cikin gaskiya da amana, har da tsabar kuɗi, tikitin ragi a tallace-tallace da katunan biyan kuɗi na kamfani
- Ka hana zamba da gurɓataccen wakilci da taimakawa haɗarin kauce wa biyan haraji ta ƙoƙarin tantance da gaskiya da sahihancin bayanan kuɗi, kamar dai da’awar kuɗin, daftarin masu kawo kaya da kuma rahotanni masu gudanarwa
- Yi biyayya ga dukkan dokokin da ke aiki, matakan kulawa da manufofin Meta da suka shafi ajiye bayanai da riƙe bayanai.

Ƙarin jagoranci:

- Dokar Samowa da Sayo Kaya Ta Meta ta Duniya
- Dokar Tafiye-tafiye da Ɓatar da Kudi ta Duniya
- Dokar Yaƙi da Cin Hanci
- Hukumar Ba Da Izinin Amincewa
- Dokar Kwangila
- Dokar Tikitin Talla

**T:**
Tsarin kasafin kuɗi yana kusa da aukuwa. Ina cikin Tawagar Lissafa Kuɗin Haraji sannan na damu matuƙa da buƙatar tawagar asusun abokin hulɗar mu. Sun kira ni suka tambaye ni idan zan iya dawo da wani ɓangare na harajin tallace-tallace daga abun da ake tsammani a wannan yanki kuma sun dage cewa a sanya ta a yanki na gaba. Bayanansu ba su gamsar ba kuma ba su son bayani dalla-dalla. Me ya kamata in yi?

**A:**
**Ka yi gaskiya da ka nuna damuwa. Yana da matuƙar muhimmanci a tanadi kuɗin haraji na daidai lokacin shekarar kasafin kuɗi don a tabbatar da sahihanci da gaskiyar asusun Meta da kuma adana kuɗaɗen jama'a. Ka tambaye su don su fayyace tare da ƙarin bayani. Idan har yanzu kana da damuwa game da ko akwai izini soke kuɗin shiga da dacewa, za ka iya ɗaukaka damuwarka zuwa ga manajanka ko wani mamba na Tawagar Ɗabbaƙawa da Ɗa'a.**

**T:**
Mai samar da kayanmu ya kira ni ya nemi mu biya takardar biyan kuɗinsu ta gaba a wani a susu na ƙetare. Ba su fayyace dalili ba ko da yake sun ambaci wani abu game da zai taimaka musu a sarrafa harajinsu na cikin gida. Ban nutsu da wannan ba - ya kamata na yi?

**A:**
**ƙari a kan haɗurra kamar alasta kuɗin haram ta hanyar biyan kuɗi ga asusun ƙetare, a nan zai iya zama masu samar da kaya suna ƙoƙarin ɓoye kuɗin shigarsu ne su kauce wa biyan haraji. A wasu ƙasashe kamar Ingila, Meta da ɗaiɗaikun ma'aikata za su iya tuhumarsu da aikata laifin taimaka wa kauce wa biyan harajin wasu can daban. Taimakawa zai iya faruwa ko da kuwa ta ƙin kula buƙatar da ake zargi ne. Ka tambayi masu kawo kaya me ya sa suke buƙatar wannan sauyin kuma kada ka aiwatar da wani biyan kuɗi har sai ɗaukaka wannan zuwa ga manajanka ko Sashen Kuɗi ko Ɗabbaƙawa da Ɗa'a.**



# Kada ka shiga a cinikayyar yankan baya

**Ba ma amfani ko raba bayanan da ba na kowa da kowa ba game da Meta ko wasu kamfanoni domin dalilan kasuwanci saboda yin hakan karya doka ne kuma zai yi illa ga dangantakar da ke tsakanin Meta da masu saka hannun jari da masu sa ido da kuma jama'a.**

Mun ɗauki ƙudurin kare bayanan da aka ba mu amanarsu, musamman bayanan da ba na bainar jama'a ba game da Meta ko wani kamfanin, da wasu lokutan ake kira bayanan "ciki." Don samun jagoranci game da abubuwa da suke ƙunshe cikin bayanan da ba na gama-gari ba da wasu dokoki game da kasuwanci, yi bitar Dokar Cinikayyar Yankan Baya.

Yin Kasuwancin tsaro a yayin sarrafa bayanan da ba na kowa da kowa ba, wanda ake kira da "cinikin yankan baya" ko samar wa da wani ɗan'uwa ko aboki ko kowane mutum da wata "shawara" a kan bayanan da ba na kowa da kowa ba, karya doka ne.



## Hana cinikayyar yankan baya yana nufin muna:

- Kada ka yi kasuwanci da tsaron Meta ko wani kamfani na jama'a lokacin da ake sarrafa bayanan da ba na kowa da kowa ba game wannan tsaron
- Kada a karɓa ko bayar da "shawarwari," a lokacin da aka sadar da wasu bayanai da ba na gama-gari ba game da Meta ko wani kamfani zuwa ga wani mutum wanda alhakinsa ne ya adana bayanan a asirce
- Kare bayanai da ba na kowa da kowa ba daga fita ko bayyanar ba zata, a ciki da wajen Meta, har ma da yin taka tsantsan wajen yin hira a muhallan jama'a
- Yi bita tare da biyayya ga Dokar Cinikayyar Yankan Baya ta Meta—akwai wasu dokoki da ya kamata ka sani dalla-dalla
- Tambayi **Trading@** idan muna da shakku ko tambayoyi—bayanan da ba na kowa dakowa ba suna da sarkakiya mun san cewa za a iya samun tambayoyi

Karin jagoranci:

- **Dokar Cinikayyar Yankan Baya**
- **Kalandar Zangon Cinikayya**
- **Trading@**

Ina son yin kasuwancin hajar Meta. Ba ni da wasu bayanan da ba na bainar jama'a ba game da Meta. Yaushe zan yi kasuwanci?

Za ka iya tallata hajar Meta ne kaɗa a yayin da aka buɗe damar tallata haja na wata uku-uku (matsawar ba ka riƙe da bayanan da ba na kowa da kowa ba) ko ta hanyar amintaccen tsarin kasuwanci na10b5-1. Gabaɗaya dai, muna buɗe damar tallata haja a yini na biyu na ranakun kasuwanci bayan an fitar da kwanan watan samun riba na rabin zango, damar tana nan buɗe mafi yawanci har zuwa ranar ƙarshe na watan tsakiya na ɗaya bisa huɗun shekara, duk da yake waɗannan kwanaki za su iya sauyawa. Kafin yin kasuwanci, ya kamata ka yi bitar Dokar Cinikayyar Yankan Baya ɗinmu da kuma Kalandar Zangon Cinikayya akan Shafin Mutane.



# Ka yi sadarwa a bayyane tare da faɗin gaskiya

## Muna nazari da kula kan yadda muke haɗuwa da kuma yin sadarwa tare da duniya.

A matsayin Ma’aikatan Meta, duk abin da muka faɗa kuma muka yaɗa yana tasirin akan ɗaiɗaikunmu da kuma a kan Meta. Kalamanmu na da matuƙar muhimmanci, ko a wurin taro ne, a shan gahawa, tafiya tare ko sadarwa ta yanar gizo. Mun yi amanna cewa dandalin yanar gizo na ƙarfafa gaskiya, sadarwa a bayyane da fahimtar cewa bayanai na saurin yaɗuwa inda ba a zata. Don haka, yana da kyau mu ɗan numfasa kafin mu yi wata magana don kauce wa rashin fahimta tare da barin a saurari kokenmu.

## Yin sadarwa a bayyane tare da faɗin gaskiya na nufin muna:


- Masu bayyanawa, da gaskiya, da riƙon amana, da fara’a da kuma ƙwarewa a kan sadarwa ta waje da ta cikin gida
- Ba sa juya magana ƙarya ko yin ƙage ko kalaman ɓata suna game da wasu
- Suna riƙe bayanan sirri na Meta yadda ya kamata (duba Kare Bayanan Sirri na Meta don ƙarin bayani)
- Suna fayyacewa a lokacin da suke rubuta a kafar sada zumunta cewa ra’ayin ƙashin kansu ne, kada mutane su ɗauke cewa muna magana ne a madadin Meta, sai dai idan an ba mu izinin yin hakan
- A tabbata cewa amfani da adana sadarwa ta kasuwanci da muke yi sun yi daidai da manufofin Meta
- Sanya kayayyakin Kamfani kan damarmakin waje masu tasiri da neman amincewa kamar yadda aka buƙata don duk wani yin magana da rubuta mu’amaloli
- Ka tuna ka aika da neman ‘yan jaridu game da dukkan batutuwan da suka danganci kasuwancin Meta wanda za ka yi magana a kai zuwa ga **Press@** Bai kamata ka yi mu’amala da ‘yan jaridu ba a madadin ko ka ba da shawara ko bisa zato ka yi magana a matsayin wakilin Meta. Dokar ba ta kuma ba ta nufin hana mambobin al’ummarmu da yin mu’amala da ‘yan jaridu a ayyukan da suka shafi kariya ko duk wani ma’aikaci don tattauna albashi ko alfanu ko sharuɗɗa da dokokin aiki a Amurka. Ba kuma ana nufin ya sauya haƙƙoƙinka ko Nauye-nauyen da ke kan Meta na dokokin da suka dace, haɗi da waɗanda suka danganci kwarmato da sirrin bayanai

Ƙarin jagoranci:

- **Dokar Ayyuka Na Waje**
- **Dokar Sadarwar Na’ura**
- **Abin da ake tsammani na Tafiya tare da Al'umma**
- **Dokar Naɗar Sauti ta Duniya**
- **Press@**

Koyaushe ka yi wa kanka waɗannan tambayoyi kafin ka danna **aika** ko **wallafa** da kuma kafin ka yi magana:

"Yaya wasu za su ji idan suka karanta wannan?" da "Yaya zan ji idan wannan ya shiga hannu jama'a?"



**T:**
Na shiga wani zauren tattaunawa ta yanar gizo game da Basirar Kwamfuta (AI) a inda ake girmama ni saboda ƙwarewata. Wani shahararren marubuci kuma wanda ya assasa shafin buloga na masana'ant ya tuntuɓe ni kuma ya gayyace ni ganawa a wani ɓangare na abun da zai fito a shafi. Ina shauƙin wannan ganawar matuƙa, shin akwai buƙatar in nemi shawarar wani kafin in amsa?

**A:**
**Muna alfahari matuƙa da abokanan aiki a Meta za mu taimaka musu wajen tallata basirarsu. Kafin ka karɓi gayyatar, ya kamata ka mika buƙatarka zuwa ga tawagar Sadarwar Waje don su tantance idan wannan damar ta magana ta dace. Suna ƙarin jagora idan har an aminta da damar.**

**T:**
Ina matuƙar shauƙi game da aiki a fannin fasaha kuma zan so in yaɗa ƙwarewata ta aiki a masana'antar fasaha kuma in tallafa wa wasu waɗanda suke yin irin haka. Ina tunanin ƙirƙirar tashar YouTube, rubuta littafi/bulog,muƙala, ko amincewa da wasu da suka yaɗa ƙwarewarsu a waɗannan hanyoyi. Akwai buƙatar in fara haɗuwa da wani?

**A:**
**Abu ne mai kyau cewa kana shauƙi game da aiki a fannin fasaha kuma ina son yaɗa ƙwarewarka ga wasu. Kafin ka fara waɗannan ayyuka, ya kamata ka miƙa wata buƙata don samin amincewa a ƙarƙashin Dokar Mu'amala ta Waje. Dole a miƙa buƙata ga kowace mu'amala da kai tsaye suke da dangantaka da Meta ko masana'antar ƙere-ƙeren fasaha. Za a iya samun ƙarin jagoranci idan an amince da damar, za ka iya samun ƙarin bayanai a cikin Dokar Sadarwar Waje. Kafin fara aikin sa wa a hanya a hukumance ko matsayin ba da shawara ga wasu mutane ko kamfani, ka miƙa buƙatar saɓanin muradu ta hanyar Kayan aiki Saɓani. Za ka iya samun ƙarin bayani a Dokar Cin Karon Muradu da kuma a kan Wiki Na Saɓani.**

# Ka hana cin hanci da rashawa

## Ba mu shiga cikin cin hanci da rashawa kuma mu gudanar da kasuwanci a fadin duniya ta amfani da kyawawan ɗabi'u.

Mu tsaya ƙyam don yaƙar duk wasu na'ukan cin hanci, har ma da bayar da ko karbar rashawa, toshiyar baki da sauran biyan kuɗi da bai dace ba. Cin hanci yana raba kan al'ummomi, ya wargazar da buɗaɗɗun kasuwanni sannan ya yi zagon ƙasa ga ƙokarin Meta na samar da damar tattalin arziki.

A matsayin kamfanin duniya, alhakin Meta ne ta taimaka wajen kawar da cin hanci a duniya ta ayyukanmu da misalai. Mu zabi rasa kasuwanci da a akan mu same shi ta hanyar cin hanci da rashawa, toshiyar baki ko biyan kuɗi da bai dace ba.



## Hana cin hanci da rashawa na nufin muna:

- Biyayya ga wasiƙa da kuma ƙokarin dokokin yaƙi da cin hanci da na yaƙi da rashawa da na yaƙi da toshiyar baki a duk lokacin da muke yin kasuwanci, har da Hukumomi da ke Yaƙi da Cin Hanci da Rashawa na Ƙasashen Waje (FCPA) da U.K. Dokar Karɓar Rashawa.
- Kada ka bayar da cin hanci ko toshiyar baki, ko wani abu mai daraja, ga ɗaiɗaikun mutane ko jami'in gwamnati don ya yi maka wani tasiri ba bisa ƙa'ida ba—ko idan ta bayyana zai iya tasiri—a kasuwanci ko hukuncin gwamnati
- Ƙi amincewa da duk wani tayin cin hanci, toshiyar baki ko wani nau'in biya ko alfanu da aka niyyar yin tasiri a kan yadda muke yanke shawarwari a Meta
- Da cikakkiyar masaliya game da mutanen da muke kasuwanci da su da kyau don mu gano ko dai jami'an gwamnati ne
- Yi bita da kyau ka zaɓi mutum na uku, mai ɗabi'a, mai gaskiya cancantacce kada ka yi amfani da su wajen aikata abun da bai dace ba (dubi Ingantacciyar Haɗin Guiwa da Wasu Daban)
- Yanke shawarwarin ɗaukar haya ta la'akari da takardun ɗan'takara, ilimi, fasaha da ƙwarewar aiki—kada ka ba da wani fifiko da bai dace ba saboda wani dalili da bai dace ba, kamar amfanar da kwastoma ko jami'in gwamnati
- Adana ingantattunbayanai da lissafi (dubi Jagora a Mutunta Hadahadar Kudi)

Ƙarin jagoranci:

- **Dokar Yaƙi da Cin Hanci**
- **Dokar Kyauta da Nishaɗantarwar Kasuwanci**
- **Dokar Tafiye-tafiye Da Kashe Kudi ta Duniya**

**T:**
Meta na yunƙurin buɗe wata cibiyar bayanai a ƙoƙarin bunƙasa kasuwanni inda ake samun hadin yanar gizo da sauri. A matsayin manajan aiki na Meta, an ɗaura mini alhakin kula da matsalolin da aka ba da izini da mahukuntan ƙananan hukumomi. Wani jami'in ƙaramar hukuma ya bayyana cewa zai iya hanzarta hanyar ba da izini da ‘yan kuɗi kaɗan da za a sau ɗaya. Ko zan iya biyan kuɗi?

**A:**
**Jami'in ƙaramar hukuma yana neman a taimaka masa ko “sauƙaƙa” biyan kuɗi don hanzarta samun izini. Mafi yawan dokokin yaki-da-rashawa sun haramta hatta ƙananan gudanar da biyan kuɗi-haka ma Meta. Kada ka biya kuɗin ka tuntuɓi sashen Shari’a ko na masu Ɗabbaƙawa da Ɗa’a cikin gaggawa don neman taimako.**

## Ka tuna, tafiya da sauri ba ya nufin tafiya cikin rashin ɗa’a.



## Jar tutar cin hanci

Meta tana da manufar aiki kawai da wasu daban waɗanda ke da irin ɗabi'unmu na kasuwanci Muna sa ran Ma'aikatan Meta da wasu daban su ɗaukaka ayyukan tuhuma ko jar tuta zuwa ga sashen Shari'a ko Ɗabbaƙawa da Ɗa'a. Ka sanya ido ga misalai masu zuwa:

### Tuhuma a lokacin farawa

- Zarge-zarge game da rashin ɗa'a ko biyan kuɗi da bai dace ba na yanzu ko wanda ya shuɗe.
- Ƙin biyayya da miƙa wuya ga dokokin yaƙi da rashawa har ma da kwangilolinmu
- Ƙin gano mamallaka kasuwanci, abokanan hulɗa ko shuwagabanni
- Alaƙar kasuwanci ko 'yan'uwantaka ga jami'in gwamnati a matsayi da za a amfanar da Meta
- A nemi ɓoye shaida ko kuma dangantakar ta zama a asirce
- An zayyana a jerin sunayen da gwamntai ta dakatar

### Bayarwa ko karbar kayayyaki masu daraja da ba su dace alfanu da bai dace

- Samar da kyaututtuka ko nishaɗantarwa ga jami'an gwamnati da suke saɓa wa Dokarnu ta Yaƙi da Cin Hanci
- Buƙaci ka ba da gudunmuwa ga ƙungiyar jin ƙai don gudanar da aikin gwamnati

### Diyya/littattafai da fayil maras inganci

- Neman gabatarwa sama da farashin kasuwa ko sama da yadda aka saba biyan ayyuka
- Neman biyan sha yanzu magani yanzu
- Ƙin adana yadda aka ɓatar da kuɗi da kyau ko nema a shirya daftari marar inganci, kwangiloli ko sauran adanawa
- Kashe kuɗi ba bisa ƙa'ida ba "ba tare da adanawa ba"
- Neman biyan tsabar kuɗi, ta mutum na uku ko ga sunan asusun da ba su da alaƙa ko muhalli
- Sakacin kula na cikin gida ko al'adar adana bayanai

### Ɗaukar aiki ko miƙa shaida mai alamar zargi

- A nemi ɗaukar hayar jami'in gwamnati ko ɗan'uwa a wani matsayi a Meta
- Ɗaukar hayar ma'aikacin wucin gadi da zai taimaka a samu kwangila daga gwamnati
- Mutum na uku da jami'in gwamnati ya ba da shawara a kai

# Bayarwa da karɓar kyaututtuka da nishaɗantarwa

## Muna sanya hannun jari a dangantakar kasuwancinmu amma ba ma karɓa ko bayar da kyaututtuka, nishaɗantarwa

Bayyana godiya ga abokanan hulɗa ko mutum na uku na ƙarfafa dangantakarmu ta kasuwanci idan aka aiwatar da ita yadda ya kamata. Musayar kyaututtuka, nishaɗantarwa ko karamci ta don a yi tasiri kan yanke shawarwarin kasuwanci ba bisa ƙa'ida na lalata da haifar da sakamakon kasuwanci da ba zai fara lura da al'ummar da ke amfani kayayyaki da ayyukan Meta ba.



## Bayarwa da karɓar kyaututtuka da nishaɗantarwa na nufin mu:

- Bayar da kyaututtuka na al'ada masu kyau, nishaɗantarwa ko duk wani abu mai wata daraja a inda ake da dalilin halartaccen kasuwanci inda kyautar ba ta haifar da bayyanar rashin dacewa
- Bi wasu jagorori na musamman akan shari'a don bayar da wasu abubuwa masu ƙima ga jami'an gwamnati ka kuma nemi izini daga Sashen Ɗabbaƙawa da Ɗa'a, idan da buƙatar hakan
- Nishaɗantar (ko nishaɗantarwa daga) wani daban a cikin dalili da manufa mai kyau (m.s., abinci mai kyau bukukuwan wasanni ko na al'ada duk an yarda da su gabaɗaya, amma ban da kurme a sararin samaniya da gidan caca), kada ka samar da gurɓataccen tunani saboda yanke shawara nan gaba Ka karɓi kyaututtuka da ke da daraja ƙasa da dalar Amurika 200 , wadda ta dace, ta al'ada cikin kyakkyawar manufa da ba za su bayyana a yanke shawara nan gaba ba.
- Kada ka karɓi ko bayar da tsabar kuɗi, daidai da (m.s., kyautar kati) ko bashi
- Tuntuɓi **Kyauta da Nishaɗantarwar Kasuwanci** don samun amincewa daga sashen Ɗabbaƙawa da Ɗa'a idan aka buƙata kafin ba da wani abu mai daraja ga jami'an gwamnati

Ƙarin jagoranci:

**Dokar Kyauta da Nishaɗantarwar Kasuwanci**

**Dokar Yaƙi da Cin Hanci**

**Dokar Tafiye-tafiye Da Kashe Kudi ta Duniya**

## Tambayoyi da za ka yi wa kanka yayin bayarwa ko karɓar kyaututtuka da nishaɗantarwa

1. Shin ina bin manufofin Meta, da suka haɗa da iyaka ga jami’an gwamnati?

2. Ko ya dace ta la’akari da al’ada da dokokin kamar hukuma?

3. Ko tana samar da halataccen dalilin kasuwanci?

4. Ko tana kauce ma haɗarin ko tunanin nuna bambanci ga yanke shawara nan gaba?

5. Ko hakan ya kauce wa tunanin ɗabi’a marar kyau?

Idan amsar ɗaya daga cikin waɗannan tambayoyi ta kasance “a’a” ce, me yiyuwa ne kyautar ko nishaɗantarwa ba ta dace ba don haka kada ka bayar ko ka karɓe ta.

**T:**
Ɗaya daga cikin masu kawo kaya ga tawagata ya aiko wa tawagata da katon ɗin barasa ba zata, ba tare da sanarwa ba. Na tuntubi mai kawo kayan don in yi masa godiya kuma in samu ƙarin bayani game da kyautar su. Ta bayyana mai kawo kayan yana tsakiyar wata yarjejeniyar kwangila tare da wata tawagar Meta kuma yana fatan zan iya taimakawa ya sami ƙarin bayanai game da tsarin. Tun da na san hakan, ba ni da tabbacin ko in karbi barasar.

**A:**
**Duk da cewa darajar farashin inabin bai kai dala 200 ba, karɓar ta ba zata a lokacin da mai kawo kaya ke neman tandar sabuwar kwangila ga Meta zai sanya mai kawo kaya ya kyautata zaton za ka yi tasiri wajen yanke shawara wajen zaɓar mai kawo kaya a wannan kwangila da ke tafe. Tun da babu tabbacin cewa an aiko da barasar ce da kyakkyawar manufa, sai ka tuntuɓi masu sashen Ɗabbaƙawa da Ɗa’a don tattaunawa kafin ka karba da kuma raba ta ga tawagarka.**

# Ka yi mu'amala da gwamnati da shugabannin siyasa cikin mutuntawa

## Muna hulɗa mai ma'ana da sanin ya kamata tare da gwamnatoci da shugabannin siyasa don ƙarfafa manufofin Meta na kawo duniya kusa da juna.

Yaɗuwar Meta a faɗin duniya da ƙirƙire-ƙirƙire na nufin cewa akai-akai za mu riƙa lura da sababbin dokoki da matakan kula da aka gabatar. Muna hulɗa da tunani, ɗabi'a da ladabi tare da zaɓaɓɓun jami'ai da masu gudanarwa don ciyar da manufar Meta da kare haƙƙin waɗanda muke ƙarfafawa. Haka kuma muna hulɗa da jam'iyyun siyasa da 'yan takara don taimaka musu su yi amfani da dandamalan Meta, amma muna yin hakan ne ba tare da gyon bayan wani ɓangare ba, inda muke ɗaukar dukkan ɓangarorin a matsayin ɗaya, muna girmama haƙƙokin ɗan Adam tare da tsayawa kan imaninmu na cewa muna aiki ne ga kowa.

Mun yi imanin cewa Ma'aikatan Meta suna da ikon shiga harakokin farar hula da na siyasa a ƙashin kansu a bayan fagen aiki mutaƙar dai an rarrabe ta da Meta.



## Yin mu'amala da gwamnati da shugabannin siyasa cikin mutuntawa na nufin muna:

- Barin abokanan aiki da ke da ƙwarewar da ake buƙata da zini su tuntuɓi jami'an gwamnati game da doka, majalisa, gudanarwa ko abubuwan da suka shafi lamurran zaɓe
- A yi biyayya ga Dokar Kamfani ta Yaƙi da Cin Hanci da Dokar Ayyukan Siyaya da na Kamun Kafa, ka yi magana da jami'an gwamnati da gaskiya kuma ka amsa tamboyoyinsu a kan lokaci da gaskiya
- Ka goyi bayan jam'iyyun siyasu da cibiyoyinsu da ke da alaƙa da yin amfani da kayayyakin Meta ba tare da tsaka tsaki ba kuma kada ku taɓa nuna fifiko ga wani ɓangare a kan wani.
- Yi biyayya ga dokoki da ke da alaƙa da lallashin bayyanawa da yekuwar iyakance kuɗi kamar yadda ake buƙata a kowane ɓangare
- Kada ka yi amfani da kayayyakin kamfani ba bisa ƙa'ida ba ko lokaci don ka goyi bayan ayyukan siyasa na ƙashin kanka
- Bari a fayyace dalla-dalla cewa, a duk lokacin da muka shiga siyasa a matsayin yan kasa masu zaman kansu, ra'ayinmu da ayyukanmu namu ne kanmu, ba na Meta ba ne

Karin jagoranci:

- Ayyukan Siyasa da Dokar Bibiya
- Dokar Yaƙi da Cin Hanci
- Abin da ake tsammani na Tafiya tare da Al'umma

**T:**

Ni mai bincike ne a kan dokokin jama'a kuma na mayar da hankali wajen daidaita fiber oftics. Na samu labarin cewa abokin aikin ɗan'uwana ya samu sabon aiki a hukumar gwamnati da ta shafi masu samar da intanet da kebul na ƙarƙashin ƙasa. Na yanke shawarar tambayar ɗan'uwana don gabatarwa saboda ina ganin zai zama mai ban sha'awa don ƙarin sani game da aikinta da yadda hakan zai iya shafar Meta. Shin wannan shawara ce mai kyau?

**A:**

**Idan ka yi wata hulɗa da abokin ɗan'uwanka kuma kuka yi magana game da Meta, za ta iya haifar da kamun-ƙafa, aiki da ake gudanar da sarƙaƙiya. Ya kamata ku tuntuɓi tawagar Ɗabbaƙawa da Ɗa'a da kuma Tawagar Dokar Jama'a, don samun jagoranci.**

**Masu kula da Ɗabbaƙawa da Ɗa'a za su iya ba da shawara a kan ko dokokin kamun ƙafa na gida suna da tasiri ko kuma ya kamata a kauce kai tsaye daga dukkan tattaunawa da ke da alaƙa da aiki.**

**Tawagar Dokar Jama'a suna da ƙwarewa da dangantakar da ake buƙata su yi hulɗa da gwamnati.**



# Samar da duniya mafi nuna kulawa, mai ɗorewa

**Muna ƙarfafa mutane don ƙirƙirar ingantacciyar, duniya mai ɗorewa ta hanyar ayyuka, kayan aiki da albarkatu waɗanda ke da tasirin gaske na duniya.**

A matsayinmu na kamfani mai tasiri a duniya, mun mayar da hankali ga kawo sauyi—ta hanyar ayyukanmu da kuma ƙarfafa wasu. Muna bunƙasawa da rarraba hanyoyin magance matsala ɗorarriyar duniya, kuma muna kusantar da al'umma ga juna ta tasirin kayan aiki na zumunta da ke samar da al'ummomi managarta, masu ƙaunar juna.



## Samar da wata duniya mai nuna kulawa, mai ɗorewa yana nufin muna:

- Girmamawa tare inganta haƙƙoƙin ɗan adam, har da tallafawa ingantaccen yanayin aiki da hana fataucin mutane a duk faɗin Meta da hanyoyin sadarwar Meta
- A haɓaka haƙƙoƙin fararen hula da kuma ƙwarewar tsirarun al'umma a dukkan dokoki, da ayyuka da kayayyaki ta yadda dukkan al'umma za su iya fafutuka a kan fasahohinmu
- Tallafa tare da saka jari a ƙungiyoyi da ke bunƙasa adalcin zamantakewa da na bambancin launin fata
- Yi ƙoƙari wajen samar da iskar gas mai kyau a dukkan faɗin duniya inda Meta ke aiki kuma ka zama mai ba da goyon baya 100% ta hanyar sabunta makamashi
- Bin ƙa'idojin tsari mai ɗorewa da cikakkun ƙa'idoji da tantancewa a cikin ofisoshin Meta da cibiyoyin bayanai
- A sake amfani, a cakuɗa a kuma ɗauki tsari mai taƙaitacciyar hasara a cikin ofisoshin Meta da shagunan shan shayi
- Samar da kayan aiki, kamar Ba da Sadaka, Kai Agaji a Lokacin Rikici da Gudummawar Jini, don ba mutane dama su goyi bayan buƙatunsu da abubuwan da suke bege
- Ka samar da damar shiga intanet, fasaha da dandalin Meta ga kowa da Kowa a faɗin duniya
- Tallafa wa al'ummomin da ke hulɗa da jama'a ta hanyar haɓaka kayan aiki don taimaka wa mutane samun ilimi game da jefa ƙuri'u

Ƙarin jagoranci:

- Tasirin Zumuntar Meta
- Ɗorewar Meta
- Haƙƙoƙin Fararen Hula
- Dokar Tallafi da Bayarwa
- Dokar Kare Haƙƙin Ɗan Adam
- Dokar Albarkatun Ƙasa

# Ƙudurin kare haƙƙin ɗan Adam na Meta

## Meta ya kasance a koyaushe game da kawo tasirin zamantakewa mai alfanu. Ƙoƙarinmu na girmama haƙƙin ɗan Adam ya taimaka wajen bayyanawa da ƙarfafa wancan tasirin.

Meta ta himmatu wajen girmama dukkan haƙƙokan ɗan Adam da aka amince da su a duniya. Waɗannan sun haɗar da haƙƙin sirrantawa da 'yancin faɗin albarkacin baki da sauran haƙƙoƙi kamar yadda aka bayyana a Dokar Haƙƙin Ɗan Adam ta Ƙasa da Ƙasa aka kuma ayyana a Dokar Ƙungiya Ƙwadago ta Duniya kan Manyan Ƙa'idoji da Haƙƙoƙi a Wurin Aiki.

Muna rayuwa da wannan himma ta hanyar dokokin al'ummar Meta da **Dokokinmu na Haƙƙin Ɗan Adam** da aikin mutuncin kayanmuda kuma yadda muke ganowa ku hana mu kuma kula da haɗarin haƙƙin ɗan adam, haɗi da haɗarin da ya danganci buƙatun gwamnati ba tare da izini ba, ko batutuwan hanyar samar da kaya ko mutane suna amfani da dandalinmu ba daidai ba don su rura rikici. Tawagoginmu na tsari da na dokoki da na gudanarwa, da na kayaya suna aiki kowace rana don su tabbatar mun girmama haƙƙin ɗan adam – kuma aiki ne mai wuya, mai muhimmin.

**Wiki Na Haƙƙokin Ɗan'adam**

# Himmar Meta ta kare haƙƙin jama'a

## Haƙƙoƙin Jama'a haƙƙoƙinn mutane ne na kada a yi musu mu'amala ta rashin adalci da nuna wariya

A matsayin kamfani, dole mu ɗaukaka ƙa'idojin haƙƙoƙin farareb hula a dukkan abin da muke yi mu kuma himmatu ga tabbatar da cewa an gina fasahohinmu da su a zuci. A wannan lokacin ne kawai za mu bunƙasa da gaske ta hanyar kayayyakinmu, mu ƙirƙiri sarari da yake inganta inganci da mutunci da damar magana ga kowa da Kowa. Wannan himmar shi ne ya sa Meta ya ɗauki hayar ƙwararru a fannin haƙƙoƙin jama'a masu zaman kansu su gudanar da bincike na shekara biyu a kan haƙƙoƙinn jama'a. A sakamakon wannan bincike, a 2020, mun kafa tawagarmu ta haƙƙoƙin jama'a - wadda jadorancin VP ne, kuma ita ce kaɗai tawagar haƙƙoƙin jama'a da aka sadaukar a masana'antar fasaha da kamfanin Amurka. Aikin Tawagar Haƙƙoƙin Jama'a ya mayar da hankali ne ga rashin nuna wariya da daidaito da adalci, waɗanda suke da muhimmanci ga gina dokoki da kayayyaki da samar da al'ada ga dukkan masu amfaninmu. idan muka yi gini da haƙƙoƙin jama'a zukatanmu za mu iya inganta dokokinmu da kayayyakinmu da al'adunmu tun a farko ta yadda al'ummomi daban-daban za su iya raba ƙwarea iri ɗaya a kan dandalinmu maimakon cusa rashin daidaiton al'umma. Mun yi imani a kan gina fasahohin da kowace al'umma za ta iya yin fafutika.

**Wiki Na Haƙƙoƙin Jama'a**

## Himmar Meta mai ɗorewa

Meta ya yi himmar mayar da hankali ga ɓangarori takwas da suke da tasiri a kan ɗaiɗaikun al'ummomi da kuma duniya:

1. **Yanayi:** rage fitar da gas daga ayyukan kamfani da kaso 75 cikin ɗari
2. **Sabunta makamashi**: mun hummatu mu tallafa wa ayyukan da suke amfani da sabunta makamashi 100 bisa ɗari
3. **Kula da ruwa**: a fifita kula da ruwa a duk inda Meta ke aiki
4. **Kirkira**: kara inganta kirkiro hanyoyin magance matsala don a samar da duniya mai ɗorewa
5. **Haɗaka**: haɗaka da wasu don gaggauta ɗaukar mataki game da batutuwan ɗorewa
6. **Hanyoyin kawo kaya masu mutunci**: tabbatar da kyakkyawan yanayin aiki da ɗorewar ayyukan muhalli
7. **Cibiyoyin bayanai masu ɗorewa**: gudanar da wasu ingantattun bayanai na kayayyakin makamashi a duniya
8. **Wuraren aiki masu ɗorewa**: kirkirar wuraren aiki masu ɗorewa waɗanda ke haɓaka walwalar ma'aikaci



# Wasu Sassa na biyayya da kuma Dokokin Ɗa’a

## Yafiya da kwaskwarima

A yanayi mawuyaci, ana iya neman yafewar wannan Kundi Babban Jami’in Ɗabbakawa na Meta na iya bayar da yafewa ga ma’aikatan Meta ban da manyan ma’aikata ko manyan ma’aikatan kuɗi. Duk wata yafewa ko gyara na wannan Kundin don memba na kwamitin Hukumar Daraktocin Meta, babban jami'i ko kuma babban jami'in kudi dole ne ya samu amincewa daga Hukumar Daraktoci kuma a hanzarta bayyana shi kamar yadda ake iya bukata bisa lamuran dokoki da ka'idoji, har da dokokin haja musayar wanda aka sanya jarin hannun jarin Meta don kasuwanci. Duk wasu gyare-gyare na kowane tanadi na wannan Kundi dole ne a yarda da shi ta Kwamitin Biyan Diyya, Kwamitin zaɓe da Gudanarwa na Hukumar Daraktocin Meta ko, idan ya dace, Kwamitin Kula da Bincike da Haɗari, kuma a hanzarta bayyana kamar yadda ake bukata bisa doka da ka'idodi.

## Saɓani

Idan aka samu Dokar ta ci karo da dokokin gida, to, ɓanagre Dokar da dokokin da ake aiki da su suka ba da dama ne kawai za a aiwatar. Daure ka tuntubi sashen Shari’a idan kana da tambayoyi game da yiyuwar Dokar ko dokar sasanta rikici. Babu wani abu a cikin Dokar Meta ko wasu ka’idoji da aka shirya don keta ko sanyaya ikon ma'aikaci na aiwatar da hakkinsa ko hakkinta a karkashi Dokar Hulɗa Kwadago ta Kasa.

Za a iya samun karin jagorancin da ya dace da yankinku ko ƙasarku a kan Wiki, kuma za ta yi nasara a kan kowane irin rashin daidaito da jagorancin da ke kunshe cikin Dokar.

A yanayin da aka sami rashin daidaito tsakanin samfurin Ingilishi na wannan Dokar da kowane nau'i na Dokar da aka fassara, samfurin Ingilishi za a yi aiki da shi gwargwadon yadda doka ta ba shi dama.

## Horaswa

Horaswa tana da mahimmanci don tabbatar da cewa Dokar da manufofin Meta waɗanda aka ambata a ciki cewa su ne kan gaba a ayyukanmu na yau da kullum. Wani dandali ne wanda bayanan da ke cikin wannan Dokar tana da mahimmin bangare na Ma'aikatan Meta tare da manufofin Meta. Don haka, duk ma’aikatan Meta dole ne su kammala horon da ake bukata da aka ɗora musu, gami da horo kan Doka da kuma manufofin Meta kamar yadda ake bukata, kuma rashin yin hakan na iya jawo daladabtarwa ko dakatar da kasuwanci.

# Cimma manufarmu cikin mutuntawa, alhakin kowa da kowa ne

A Meta, akwai buƙatar mu himmatu wajen riƙo da kuma ɗora wa kanmy nauyin babban tsari saboda irin tasirinmu da kuma jama’a da muke cimma, ta haka za mu iya samar da fasahohin da ke da kyakkyawan tasiri ga jama’a, mu ba jama’a kariya tare da aiki da kowa. Dukkanmu mun yi tarayya wajen cimma manufofinmu.

Da wannan tunanin da kuma mayar da hankali kan gini yadda ya kamata, zamu iya ci gaba da kirkirar a tsakanin junanmu, abokanmu da kuma biliyoyin mutanen da muke yiwa aiki a duniya.



Meta